Bayanan kula: translate@mokhtasr.com



الجزء ٢٧ الحزب ٥٣

۞ قال فما خطبكم أيها المرسلون ٣١ قالوا إنا أرسلنا إلى قوم
مجرمين ٣٢ لنرسل عليهم حجارة من طين ٣٣ مسومة عند ربك
للمسرفين ٣٤ فأخرجنا من كان فيها من المؤمنين ٣٥ فما وجدنا
فيها غير بيت من المسلمين ٣٦ وتركنا فيها آية للذين يخافون
العذاب الأليم ٣٧ وفي موسى إذ أرسلناه إلى فرعون بسلطان
مبين ٣٨ فتولى بركنه وقال ساحر أو مجنون ٣٩ فأخذناه وجنوده
فنبذناهم في اليم وهو مليم ٤٠ وفي عاد إذ أرسلنا عليهم الريح
العقيم ٤١ ما تذر من شيء أتت عليه إلا جعلته كالرميم ٤٢
وفي ثمود إذ قيل لهم تمتعوا حتى حين ٤٣ فعتوا عن أمر ربهم
فأخذتهم الصاعقة وهم ينظرون ٤٤ فما استطاعوا من قيام
وما كانوا منتصرين ٤٥ وقوم نوح من قبل إنهم كانوا قوما
فاسقين ٤٦ والسماء بنيناها بأيد وإنا لموسعون ٤٧ والأرض
فرشناها فنعم الماهدون ٤٨ ومن كل شيء خلقنا زوجين
لعلكم تذكرون ٤٩ ففروا إلى الله إني لكم منه نذير مبين ٥٠
ولا تجعلوا مع الله إلها آخر إني لكم منه نذير مبين ٥١



**(31) Sai Annabi Ibrahim (A.S) ya cewa Malaikun: "Me yake tafe da ku? Kuma me kuke so?"**

**(32) Sai Mala'ikun suka bashi amsa da cewa: "Haqiqa mu Allah ya aiko mu zuwa ga mutane masu laifi, waxanda su ke aikata miyagun laifuka". (33) Domin mu sako musu duwatsun yunvu masu qarfi a kansu. (34) Dawatsun da aka yi musu alama daga wurin Ubangijinka - Ya kai Annabi Ibrahim -. duwatsun da ake sako su ga masu qetare iyakokin Allah, masu kutsawa cikin kafirci da savon Allah. (35) Sai muka fitar da muminai, waxanda suka kasance cikin wannan alqarya, daga cikin mutanen Annabi Luxu, don gudun kada azabar da zata sami masu laifi ta same su.**

**(36) Kuma kaf a cikin wannan alqarya bamu samu gidan musulmi guda xaya ba, sai gidan Annabi Luxu (A.S). (37) Kuma mun bar guraben azaba a cikin wannan alqarya ta mutanen Annabi Luxu, waxanda zasu nuna azaba ta afkawa wannan alqarya, domin masu tsoron azaba mai ciwo su xau izina daga waxannan gurabe, baza su yi irin aikinsu ba, don su tsira daga irin wannan azabar.**

**(38) Dangane da Annabi Musa lokacin da muka aika shi, zuwa ga Fir'auna da hujjoji bayyanannu. A cikin hakan akwai aya ga wanda yake tsoron azaba mai raxaxi. (39) Sai Fir'auna ya bijire daga gaskiya, yana mai tinqaho da qarfinsa da rundunarsa. Ya ce game da Annabi Musa (A.S): "Matsafi ne da yake tsafe mutane, ko kuma mahaukaci ne da yake faxar abin da baya hankaltarsa". (40) Sai muka damqe shi, shi da rundunarsa gaba xaya, muka jefa su a cikin teku, suka nutse, suka halaka. Fir'auna zai zo gobe alqiyama da abin zargi, na qaryatawa da yin da'awar allantaka.**

**(41) A cikin lamarin Adawa, mutanen Annabi Hudu, akwai aya ga wanda yake tsoron azaba mai raxaxi, a lokacin da muka aika musu iska, wadda bata xauke da ruwa, kuma bata fitar da bishiya, kuma babu wata albarka a cikinta.**

**(42) Bata barin wani rai, ko dukiya, ko waninsu face tabi ta kansa, ta bar shi kamar abin da ya lalace, ya ratattake.**

**(43) A cikin lamarin Samudawa mutanen Annabi Salihu, akwai aya ga wanda yake tsoron azaba mai raxaxi, lokacin da aka ce musu: "Ku more rayuwarku kafin ajalinku ya qare". (44) Sai suka yi girman kai ga umarnin Ubangijinsu, tare da bijirewa imani da xa'a, sai tsawar azaba ta afka musu, a yayin da suke jiran azabar, domin dama an yi musu alqawarin afkuwarta tun gabanin ta zo da kwana uku. (45) Basu iya kare kansu daga abin da ya sauka a kansu na azaba ba, kuma basu da wani qarfi da zasu kare kansu da shi daga azabar. (46) Haqiqa mun halakar da mutanen Annabi Nuhu ta hanyar nutsar da su a cikin ruwa, tun gabanin waxannan masu qaryatawar. haqiqa su mutane ne marasa yi wa Allah biyayya, don haka suka cancanci azabar Allah. (47) Sama mun gina ta, kuma mun kyautata gininta da qarfi, kuma tabbas mu masu yalwata gefenta ne. (48) Qasa kuma mun sanya ta abar shimfixawa ga mazaunanta, kai kace shimfixa ce. Madalla da masu shimfixawa mu, yayin da muka shimfixa musu ita.**

**(49) Daga dukkan komai mun halicci kala biyu, kamar namiji da mace, da sama da qasa, da tudu da teku, ko kwa tuna kaxaitakar Allah, wanda ya halicci komai guda biyu, ku tuna ikonsa.**

**(50) Don haka ku gudu daga azabar Allah zuwa ga ladansa, ta hanyar yi masa biyayya da barin sava masa. Ya ku mutane haqiqa ni mai gargaxi ne gare ku daga azabarsa. Gargaxi bayyananne.**

**(51) Kada ku sanya wani abin bauta tare da Allah, kuna bauta masa koma bayan Allah, haqiqa ni mai gargaxi ne daga gare shi, a bayyane.**

**Kaxan Daga Abin Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Imani shi ne mafi qololuwar daraja a kan Musulunci. 2 - Halakarwar da Allah ya yi wa al'ummun da suka qaryata darasi ne ga mutane gaba xaya.**
**3 - Tsoron Allah yana sa gudu zuwa gare shi ne, ta hanyar aiki na qwarai, ba wai gujewa Allah ba.**

كَذَٰلِكَ مَآ أَتَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا قَالُواْ سَاحِرٌ أَوۡ مَجۡنُونٌ
٥٢ أَتَوَاصَوۡاْ بِهِۦۚ بَلۡ هُمۡ قَوۡمٞ طَاغُونَ ٥٣ فَتَوَلَّ عَنۡهُمۡ فَمَآ أَنتَ
بِمَلُومٖ ٥٤ وَذَكِّرۡ فَإِنَّ ٱلذِّكۡرَىٰ تَنفَعُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٥٥ وَمَا خَلَقۡتُ
ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ٥٦ مَآ أُرِيدُ مِنۡهُم مِّن رِّزۡقٖ وَمَآ أُرِيدُ
أَن يُطۡعِمُونِ ٥٧ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلرَّزَّاقُ ذُو ٱلۡقُوَّةِ ٱلۡمَتِينُ ٥٨
فَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُواْ ذَنُوبٗا مِّثۡلَ ذَنُوبِ أَصۡحَٰبِهِمۡ فَلَا يَسۡتَعۡجِلُونِ
٥٩ فَوَيۡلٞ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن يَوۡمِهِمُ ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ٦٠

آيَاتُهَا ٤٩ سُورَةُ الطُّورِ تَرْتِيبُهَا ٥٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلطُّورِ ١ وَكِتَٰبٖ مَّسۡطُورٖ ٢ فِي رَقّٖ مَّنشُورٖ ٣ وَٱلۡبَيۡتِ
ٱلۡمَعۡمُورِ ٤ وَٱلسَّقۡفِ ٱلۡمَرۡفُوعِ ٥ وَٱلۡبَحۡرِ ٱلۡمَسۡجُورِ ٦ إِنَّ
عَذَابَ رَبِّكَ لَوَٰقِعٞ ٧ مَّا لَهُۥ مِن دَافِعٖ ٨ يَوۡمَ تَمُورُ ٱلسَّمَآءُ
مَوۡرٗا ٩ وَتَسِيرُ ٱلۡجِبَالُ سَيۡرٗا ١٠ فَوَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ
١١ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي خَوۡضٖ يَلۡعَبُونَ ١٢ يَوۡمَ يُدَعُّونَ إِلَىٰ نَارِ
جَهَنَّمَ دَعًّا ١٣ هَٰذِهِ ٱلنَّارُ ٱلَّتِي كُنتُم بِهَا تُكَذِّبُونَ ١٤



**(52) Irin wannan qaryatawar da mutanen Makkah suka yi, haka ma al'ummun da suka gabata suka yi, babu wani Manzo da ya zo musu daga Allah face sun ce masa: "Shi matsafi ne, ko kuma mahaukaci ne". (53) Shin ko magabata daga cikin kafirai, da waxanda suka zo daga baya a cikinsu, sun yi wasici ne a tsakaninsu a kan qaryata Manzanni? A'a, kawai dai shisshiginsu ne ya haxa su a kan haka. (54) Ya kai wannan Manzo, ka kawar da kai daga waxannan masu qaryatawa. kai ba abin zargi ba ne, haqiqa ka isar musu da saqon da aka aiko ka da shi zuwa gare su. (55) Amma kada kawar da kanka ga barinsu ya hana ka yi musu wa'azi, da tunatar da su, ka yi musu wa'azi, kuma ka tunatar da su, tabbas tunatarwa tana amfanar ma'abota imani. (56) Ban halicci mutum da aljan ba sai domin su bauta mini, ni kaxai, ban halicce su don su sanya min abokin tarayya ba.**
**(57) Kuma ba na buqatar wani arziki daga wurinsu, kuma ba na buqatar su ciyar da ni.**
**(58) Haqiqa Allah ne mai azurta bayinsa, kuma dukkansu suna buqatar arzikinsa, kuma shi ne ma'abocin qarfin da babu mai iya rinjayarsa, kuma dukkanin aljanu da mutane masu ranqafawa ne ga qarfinsa, tsarki ya tabbata a gare shi.**
**(59) Haqiqa waxanda suka zalunci kansu da qaryataka – Ya kai wannan Manzo - suna da rabo na azaba, kamar rabon da abokansu da suka gabata suke da shi, yana da lokaci iyakantacce, don haka kada su yi gaggawar neman sa, su bari lokacinsa ya yi.**
**(60) Halaka da hasara sun tabbata ga waxanda suka kafircewa Allah, suka qaryata Manzonsa, a ranar alqiyama, ranar da aka yi musu alqawarin saukar da azaba a kansu a cikinta.**

# Suratux Xuri

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Vata shubuhohin masu qaryatawa, ta hanyar gabatar da hujjoji da dalilai, domin a tilasta musu miqa wuya da sallamawa.**

**Tafsir:** **(1) Allah ya yi rantsuwa da dutsen da ya yi magana da Annabi musa (A.S) a kansa.**
**(2) Kuma ya yi rantsuwa da littafin da yake a rubuce. (3) A cikin takardu shimfixaxxu, buxaxxu, kamar littafan da aka saukar. (4) Kuma ya yi rantsuwa da xakin da Mala'iku suke raya shi da bauta a cikin sama.**
**(5) Kuma ya yi rantsuwa da sama maxaukakiya, wadda take tamkar rufi ga qasa.**
**(6) Kuma ya yi rantsuwa da teku, wanda yake cike da ruwa. (7) Haqiqa azabar Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo - mai afkuwa ce a kan kafirai, babu makawa. (8) Basu da wani mai kariya da zai kare su daga gare ta, ya hana faruwarta a gare su. (9) A ranar da sama zata yi motsi, da jujjuyawa, alamar tashin alqiyama.**
**(10) Kuma Duwatsu su tafi daga inda suke, dukkan tafiya. (11) To, halaka da hasara a wannan rana sun tabbata ga masu qaryata abin da Allah ya yi alqawari na azaba ga kafirai. (12) Waxanda suke kutsawa cikin vatanci, suna masu yin wasa, basa damuwa da wani tashin alqiyama, ko dawowa bayan mutuwa. (13) A ranar da za a tunkuxa su da qarfi da tsanani zuwa wutar Jahannama, tunkuxawa (14) Kuma a ce musu a cikin wulaqanci: "Wannan ita ce wutar da kuka kasance kuna qaryatawa, a yayin da Manzanninku suke tsoratar da ku ita".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Karantarwa:** **1 - Kafirci tafarki ne guda xaya, koda kuwa hanyoyinsa sun bambanta, ko masu yinsa, ko zamaninsu, ko wurin da suke yi ya sha bamban. 2 - Shaidar Allah ga Manzonsa (S.A.W) kan ya isar da Aiken Allah. 3 - Hikimar halittar aljanu da mutane ita ce tabbatar da bautar Allah da dukkan abubuwanta. 4 - Halin Duniya zai canja a ranar tashin alqiyama.**

أَفَسِحْرٌ هَٰذَآ أَمْ أَنتُمْ لَا تُبْصِرُونَ ١٥ ٱصْلَوْهَا فَٱصْبِرُوٓا۟
أَوْ لَا تَصْبِرُوا۟ سَوَآءٌ عَلَيْكُمْ ۖ إِنَّمَا تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ١٦
إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى جَنَّٰتٍ وَنَعِيمٍ ١٧ فَٰكِهِينَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمْ رَبُّهُمْ
وَوَقَىٰهُمْ رَبُّهُمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ١٨ كُلُوا۟ وَٱشْرَبُوا۟ هَنِيٓـًٔا بِمَا
كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ١٩ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ سُرُرٍ مَّصْفُوفَةٍ ۖ وَزَوَّجْنَٰهُم
بِحُورٍ عِينٍ ٢٠ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّبَعَتْهُمْ ذُرِّيَّتُهُم بِإِيمَٰنٍ أَلْحَقْنَا
بِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَمَآ أَلَتْنَٰهُم مِّنْ عَمَلِهِم مِّن شَىْءٍ ۚ كُلُّ ٱمْرِئٍۭ بِمَا
كَسَبَ رَهِينٌ ٢١ وَأَمْدَدْنَٰهُم بِفَٰكِهَةٍ وَلَحْمٍ مِّمَّا يَشْتَهُونَ ٢٢
يَتَنَٰزَعُونَ فِيهَا كَأْسًا لَّا لَغْوٌ فِيهَا وَلَا تَأْثِيمٌ ٢٣ ۞ وَيَطُوفُ عَلَيْهِمْ
غِلْمَانٌ لَّهُمْ كَأَنَّهُمْ لُؤْلُؤٌ مَّكْنُونٌ ٢٤ وَأَقْبَلَ بَعْضُهُمْ عَلَىٰ
بَعْضٍ يَتَسَآءَلُونَ ٢٥ قَالُوٓا۟ إِنَّا كُنَّا قَبْلُ فِىٓ أَهْلِنَا مُشْفِقِينَ
٢٦ فَمَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْنَا وَوَقَىٰنَا عَذَابَ ٱلسَّمُومِ ٢٧ إِنَّا كُنَّا
مِن قَبْلُ نَدْعُوهُ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْبَرُّ ٱلرَّحِيمُ ٢٨ فَذَكِّرْ فَمَآ أَنتَ بِنِعْمَتِ
رَبِّكَ بِكَاهِنٍ وَلَا مَجْنُونٍ ٢٩ أَمْ يَقُولُونَ شَاعِرٌ نَّتَرَبَّصُ بِهِۦ رَيْبَ
ٱلْمَنُونِ ٣٠ قُلْ تَرَبَّصُوا۟ فَإِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُتَرَبِّصِينَ ٣١

الحزب ٥٣



(15) Shin wannan abin da kuka gani ido buxe na azaba shi ma tsafi ne? Ko kuwa ba kwa ganinsa ne?. (16) Ku xanxani zafin wannan wutar, kuma ku yi fama da ita, ko ku yi haquri, ko kada ku yi haquri, duk xaya ne, haqurinku da rashin haqurinku, a yau baza a yi muku sakayya ba sai da abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya na kafirci da savo. Yayin da Allah ya ambaci sakamakon masu qaryatawa, sai kuma ya ambaci sakamakon masu gasgatawa, masu tsoronsa, ya ce: (17) Tabbas masu tsoron Ubangijinsu, ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar haninsa, suna cikin Aljannatai da ni'imomi masu girma, waxanda basa yankewa. (18) Suna masu jin daxi da abubuwan da Allah ya basu na kayan daxi, da ciye ciye, da shaye shaye, da mata, kuma Ubangijinsu mai tsarki ya kare su daga azabar wutar Jahimu, don haka sai suka rabauta da samun abin da suke nema na jin daxi, da kuma kuvuta daga rashin daxi. (19) Kuma za a ce da su: "Ku ci ku sha daga duk abin da ranku yake sha'awa, hankalinku a kwance, kada ku ji tsoron cutuwa daga abin da kuke ci ko kuke sha, sakamako ne a kan kyawawan ayyukan da kuke aikatawa a duniya. (20) Suna kashingixe a kan gadaje masu ado, a sanya su suna kallon juna, sashe a gefen sashe, kuma mun aura musu fararen mata, masu manyan idanuwa. (21) Waxanda suka yi imani, kuma 'ya'yansu suka bi su a cikin imani, to zamu riskar musu da 'ya'yansu don idanuwansu su yi sanyi, su samu farin ciki, koda kuwa basu kai iyayensu kyawun aiki ba, kuma ba zamu rage musu komai ba, daga ladan ayyukansu, kowane mutum za a tsare shi da munanan abubuwan da ya aikata, babu wanda zai xaukar masa komai daga ayyukansa. (22) Kuma muka qarawa waxannan 'yan Aljannar, da kayan marmari kala-kala, da abin da suke sha'awa na nama.

(23) Suna masu shan giya a Aljannah, wadda babu abin da yake biyo bayan shan ta, irin wanda yake faruwa a duniya, na maganganun banza, da zunubi saboda maye. (24) Yara suna kewaya su, waxanda aka hore su don yi musu hidima, kai ka ce yaran lu'u-lu'u ne wanda aka kiyaye, saboda tsabar farin fatarsu da haskenta.

(25) Sashen 'yan Aljanna ya fuskanci sashe, suna tambayar juna a kan halinsu a duniya. (26) Sai su basu amsa da cewa: "Haqiqa mun kasance a duniya, a tsakanin iyalanmu, masu jin tsoron azabar Allah ne matuqa".

(27) Sai Allah ya yi mana baiwar shiriya zuwa ga Musulunci, kuma ya tsare mu daga azaba mai tsananin zafi.

(28) Kuma haqiqa mun kasance a rayuwarmu ta duniya muna bauta masa, muna roqonsa ya kare mu daga azabar wuta, haqiqa Allah mai kyautatawa, mai gaskiya a cikin alqawarinsa ga bayinsa, kuma mai jin tausayin su, daga cikin tausayinsa gare mu ne ya shiryar da mu ga imani, kuma ya shigar da mu Aljannah, ya nisantar da mu daga shiga wuta. (29) Ya kai wannan Manzo, ka yi tunatarwa da Alqur'ani, kuma kai ba boka bane mai ganin aljanu dangane da ni'imar da Allah ya yi maka ta imani da hankali, kuma kai ba mahaukaci ba ne.

(30) Shin waxannan masu qaryatawa suna cewa ne: "Muhammad ba Manzo ba ne, kawai mawaqi ne da muke jira mutuwa ta afka masa, mu huta da shi".

(31) Ka ce da su - Ya kai wannan Manzo -: "Ku jira mutuwata, ni kuma zan jira abin da zai same ku na zaba, sakamakon qaryata ni da kuka yi".

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 -** Haxa tsakanin iyaye da 'ya'yansu a matsayi xaya, a cikin gidan Aljannah, koda kuwa aikin wasu daga cikinsu bai kai na wasu ba, don girmamawa gare su, kuma don fari cikinsu ya cika.

**2 -** Giyar lahira bata haifar da abin qi idan aka shata.

**3 -** Wanda ya ji tsoron Ubangijinsa a duniyarsa, sai ya amintar da shi a lahirarsa.

أَمْ تَأْمُرُهُمْ أَحْلَٰمُهُم بِهَٰذَآ ۚ أَمْ هُمْ قَوْمٌ طَاغُونَ ﴿٣٢﴾ أَمْ يَقُولُونَ تَقَوَّلَهُۥ ۚ
بَل لَّا يُؤْمِنُونَ ﴿٣٣﴾ فَلْيَأْتُوا۟ بِحَدِيثٍ مِّثْلِهِۦٓ إِن كَانُوا۟ صَٰدِقِينَ
﴿٣٤﴾ أَمْ خُلِقُوا۟ مِنْ غَيْرِ شَىْءٍ أَمْ هُمُ ٱلْخَٰلِقُونَ ﴿٣٥﴾ أَمْ خَلَقُوا۟
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ ۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ﴿٣٦﴾ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَبِّكَ
أَمْ هُمُ ٱلْمُصَيْطِرُونَ ﴿٣٧﴾ أَمْ لَهُمْ سُلَّمٌ يَسْتَمِعُونَ فِيهِ ۖ فَلْيَأْتِ
مُسْتَمِعُهُم بِسُلْطَٰنٍ مُّبِينٍ ﴿٣٨﴾ أَمْ لَهُ ٱلْبَنَٰتُ وَلَكُمُ ٱلْبَنُونَ ﴿٣٩﴾
أَمْ تَسْـَٔلُهُمْ أَجْرًا فَهُم مِّن مَّغْرَمٍ مُّثْقَلُونَ ﴿٤٠﴾ أَمْ عِندَهُمُ ٱلْغَيْبُ
فَهُمْ يَكْتُبُونَ ﴿٤١﴾ أَمْ يُرِيدُونَ كَيْدًا ۖ فَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ هُمُ ٱلْمَكِيدُونَ ﴿٤٢﴾
أَمْ لَهُمْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٤٣﴾ وَإِن يَرَوْا۟ كِسْفًا
مِّنَ ٱلسَّمَآءِ سَاقِطًا يَقُولُوا۟ سَحَابٌ مَّرْكُومٌ ﴿٤٤﴾ فَذَرْهُمْ حَتَّىٰ يُلَٰقُوا۟
يَوْمَهُمُ ٱلَّذِى فِيهِ يُصْعَقُونَ ﴿٤٥﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِى عَنْهُمْ كَيْدُهُمْ شَيْـًٔا
وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤٦﴾ وَإِنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ عَذَابًا دُونَ ذَٰلِكَ وَلَٰكِنَّ
أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٤٧﴾ وَٱصْبِرْ لِحُكْمِ رَبِّكَ فَإِنَّكَ بِأَعْيُنِنَا ۖ وَسَبِّحْ
بِحَمْدِ رَبِّكَ حِينَ تَقُومُ ﴿٤٨﴾ وَمِنَ ٱلَّيْلِ فَسَبِّحْهُ وَإِدْبَٰرَ ٱلنُّجُومِ ﴿٤٩﴾

ترتيبها ٥٣ — سُورَةُ النَّجْمِ — آياتها ٦٢



**(32) Shin ko dai hankulansu ne suke umartar su
da faxin: "Shi boka ne mahaukaci?!" Sai su haxa
abin da baya haxuwa ga mutum xaya, kawai dai
su mutane ne masu wuce iyaka, basa komowa ga
shari'a ko ga hankali. (33) Ko kuma suna cewa:
"Annabi Muhammad (S.A.W) shi ne ya qirqiri
wannan Alqur'ani, ba a yi masa wahayinsa ba?.
To bai qirqire shi ba, kawai dai suna girman kai
ne ga barin imani da shi, don haka sai su ce, ya
qirqire shi. (34) To idan haka ne, su zo da wata
magana irinsa, koda qirqirarra ce, idan har da
gaske suke yi a cikin wannan iqirari da suka
yi, cewa qirqirarsa a ka yi. (35) Shin ko kuwa
an halicce su ne, ba tare da wani Mahalicci da
ya halicce su ba? Ko kuwa su ne suka halicci
kansu?. Ba zai yiwu ba a samu abin halitta ba
tare da wanda ya halicce shi ba, ko kuma abin
halitta ba ne yake halitta, to me yasa baza su
bautawa Mahaliccinsu ba?. (36) Ko su ne suka
halicci sammai da qassai? Haba, kawai dai basa
sakankancewa Allah shi ne Mahaliccinsu, domin
da sun sakankance da haka da sun kaxaita shi,
kuma da sun yi imani da Manzonsa. (37) Ko
kuwa taskar Ubangijinka a hannunsu take, don
haka zasu bawa wanda suka ga dama, daga ciki
akwai Annabta, sai su ba wanda suka ga dama, su
hana wanda suka ga dama? Ko kuwa su ne masu
cikakken iko da sarrafa komai yadda suke so?.
(38) Ko suna da wani tsani da suke hawa zuwa
sama da shi ne, suna sauraron wahayin da
Ubangiji yake yi, wanda a cikinsa aka ce suna
kan gaskiya? To, duk wanda ya tava jin wannan
wahayin ya zo da hujja bayyananna, da zata gasgata ku kan da'awarku cewa kuna kan gaskiya. (39) Ko kuwa
Allah mai tsarki yana da 'ya'ya mata, waxanda kuka tsana, ku kuma kuna da 'ya'ya maza, waxanda kuke son su?.
(40) Ko kana neman wani lada ne a wurinsu – Ya kai wannan Manzo - game da saqon Ubangijinka da kake isar
musu?. Saboda haka sai aka xora musu nauyin da baza su iya xauka ba. (41) Ko kuwa suna da ilimin gaibu ne, da
suke rubutawa mutane abubuwan da suka gano na voye, su basu labaran abin da suka ga dama?. (42) Ko kuwa
waxannan masu qaryatawar suna nufin makirci ne gare ka da kuma addininka? To ka sakankan ce da Allah kawai.
Waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa su ne waxanda aka yi wa makirci, ba kai ba. (43) Ko suna da wani
abin bauta ne da gaskiya bayan Allah? Allah ya tsarkaka, kuma ya xaukaka ga barin abin da suke danganta masa
na abokin tarayya, kuma duk abin da ya gabata ba haka ba ne, kuma ba zai tava yiwu ba. (44) Kuma da a ce zasu
ga wani yanki na sama ya rufto qasa, da cewa zasu yi: "Wannan girgije ne da ya tattaru, sashensa kan sashe, kamar
yadda aka saba, don haka baza su tava wa'azantuwa ba, ko kuma suyi imani. (45) Ya kai wannan Manzo, ka rabu
da su a cikin taurin kansu da jayayyarsu, har su haxu da ranar da za a azabtar da su a cikinta, ita ce ranar tashin
alqiyama. (46) Ranar da makircinsu ba zai amfana musu da komai ba, kaxan ko da yawa, kuma ba za a taimake su
ba, ta hanyar tseratar da su daga azaba. (47) Tabbas waxanda suka zalunci kansu da yin shirka da savo, suna da
wata azaba kafin azabar ranar lahira, a duniya ta kisa da kamu a wurin yaqi. A barzahu kuma da azabar qabari,
sai dai da yawansu basu san haka ba, don haka suke tsayawa a kan kafircin su. Yayin da Allah ya bayyana vacin
abin da mushirikai suke kai, sai ya umarci Manzonsa ya daina damuwa da su, kuma ya ci gaba da yin haquri akan
qaryata shi da suke yi, ya ce: (48) Ya kai wannan Manzo, ka yi haquri a kan hukuncin Ubangijinka, da hukuncin
shari'arsa, lallai kai kana cikin kulawarmu da kiyayewarmu. Don haka ka tsarkake Ubangijinka duk lokacin da
ka tashi daga barcinka. (49) Kuma daga cikin dare ka tsarkake Ubangijinka, ka yi salla dominsa, ka yi sallar asuba
a yayin da taurari suke bada baya, haskensu yake dusashewa da hasken yini.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Xagawa sababi ce da cikin sabubban vata. 2 - Muhimmancin yin jidali na hankali a wurin tabbatar da gaskiyar addini. 3 - Tabbatar da azabar barzahu.**

# Suratun Najmi

An Saukar Da Ita A Makkah

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلنَّجۡمِ إِذَا هَوَىٰ ١ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمۡ وَمَا غَوَىٰ ٢ وَمَا يَنطِقُ عَنِ
ٱلۡهَوَىٰٓ ٣ إِنۡ هُوَ إِلَّا وَحۡيٞ يُوحَىٰ ٤ عَلَّمَهُۥ شَدِيدُ ٱلۡقُوَىٰ ٥
ذُو مِرَّةٖ فَٱسۡتَوَىٰ ٦ وَهُوَ بِٱلۡأُفُقِ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٧ ثُمَّ دَنَا فَتَدَلَّىٰ ٨
فَكَانَ قَابَ قَوۡسَيۡنِ أَوۡ أَدۡنَىٰ ٩ فَأَوۡحَىٰٓ إِلَىٰ عَبۡدِهِۦ مَآ أَوۡحَىٰ ١٠
مَا كَذَبَ ٱلۡفُؤَادُ مَا رَأَىٰٓ ١١ أَفَتُمَٰرُونَهُۥ عَلَىٰ مَا يَرَىٰ ١٢ وَلَقَدۡ رَءَاهُ
نَزۡلَةً أُخۡرَىٰ ١٣ عِندَ سِدۡرَةِ ٱلۡمُنتَهَىٰ ١٤ عِندَهَا جَنَّةُ ٱلۡمَأۡوَىٰٓ ١٥
إِذۡ يَغۡشَى ٱلسِّدۡرَةَ مَا يَغۡشَىٰ ١٦ مَا زَاغَ ٱلۡبَصَرُ وَمَا طَغَىٰ ١٧ لَقَدۡ رَأَىٰ
مِنۡ ءَايَٰتِ رَبِّهِ ٱلۡكُبۡرَىٰٓ ١٨ أَفَرَءَيۡتُمُ ٱللَّٰتَ وَٱلۡعُزَّىٰ ١٩ وَمَنَوٰةَ
ٱلثَّالِثَةَ ٱلۡأُخۡرَىٰٓ ٢٠ أَلَكُمُ ٱلذَّكَرُ وَلَهُ ٱلۡأُنثَىٰ ٢١ تِلۡكَ إِذٗا قِسۡمَةٞ
ضِيزَىٰٓ ٢٢ إِنۡ هِيَ إِلَّآ أَسۡمَآءٞ سَمَّيۡتُمُوهَآ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ
ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلۡطَٰنٍۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ وَمَا تَهۡوَى ٱلۡأَنفُسُۖ
وَلَقَدۡ جَآءَهُم مِّن رَّبِّهِمُ ٱلۡهُدَىٰٓ ٢٣ أَمۡ لِلۡإِنسَٰنِ مَا تَمَنَّىٰ ٢٤ فَلِلَّهِ
نصف الحزب ٥٣ ٱلۡأٓخِرَةُ وَٱلۡأُولَىٰ ٢٥ ۞ وَكَم مِّن مَّلَكٖ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ لَا تُغۡنِي
شَفَٰعَتُهُمۡ شَيۡـًٔا إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ أَن يَأۡذَنَ ٱللَّهُ لِمَن يَشَآءُ وَيَرۡضَىٰٓ ٢٦



## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin gaskiyar wahayi, da xaukakar inda ya fito, domin tabbatar da aqidar kaxaita Allah, da kuma vata aqidar shirka.**

**Tafsir:** **(1) Allah ya yi rantsuwa da tauraro a yayin da ya faxo. (2) Annabi Muhammad (S.A.W) bai kauce hanyar shiriya ba, kuma bai zamo vatacce ba, tabbas shi shiryayye ne. (3) Kuma baya furta wannan Alqur'ani don bin son zuciyarsa. (4) Wannan Alqur'ani ba komai ba ne face wahayi da Allah ya yi masa, ta hanyar Mala'ika Jibril (A.S). (5) Mala'ika mai tsananin qarfi ne yake koya Masa, shi ne Malaika jibrilu (A.S). (6) Mala'ika Jibrilu (A.S) ma'aboci kyakkyawar kama, sai ya daidaita a bayyane ga Annabi (S.A.W) bisa halittarsa ta ainihi, wadda Allah ya halicce shi a kanta. (7) Mala'ika jibrilu yana cikin sasasanni sama maxaukakiya. (8) Sannan sai Jibrilu ya kusanci Annabi (S.A.W) ya qara kusantar sa sosai. (9) Kusancinsa ga Manzon ya kasance gwargwadon kusancin bakin baka biyu, ko fiye da haka a wurin kusanci. (10) Sai Jibrilu ya yi wahayi ga bawan Allah Annabi Muhammad (S.A.W) abin da ya yi wahayi a gare shi. (11) Zuciyar Annabi Muhammad bata qaryata abin da idanunsa ya gani ba. (12) Ya ku Mushirikai, yanzu kuna jayayya da shi a kan abin da Allah ya nuna masa a daren da yayi Isra'i da shi? (13) Haqiqa Annabi Muhammad (S.A.W) ya ga Mala'ika Jibrilu a kamanninsa na ainihi, a wani karo na daban, a daren da aka yi Isra'i da shi. (14) A wurin magaryar tuqewa. Wata bishiya ce mai girma sosai, a cikin sama ta bakwai. (15) A wurin wannan bishiyar ne Aljannar Makoma take. (16) A yayin da abubuwa masu yawa na lamarin Allah suke lulluve wannan bishiya, wanda babu wanda ya san haqiqaninsu sai Allah kaxai. (17) Ganinsa (S.A.W) bai kauce dama ko hagu ba, kuma bai wuce inda aka iyakance masa ba. (18) Tabbas Annabi Muhammad (S.A.W) ya ga ayoyi masu girma na Ubangijinsu, da suke nuna ikonsa, a daren da aka yi Mi'iraji da shi, ya ga Aljanna, kuma ya ga wuta, da kuma wasu abubuwan daban. (19) Ya ku Mushirikai, ku ba ni labarin waxannan gumaka da kuke bautawa, Lata da Uzza. (20) Da Manata ta Uku xin biyun gumanku, ku ba ni labari, shin suna mallakar amfani gare ku ko cutarwa?. (21) Yanzu - Ya ku Mushirikai – kuna xa namiji da kuke so, shi kuma Allah mai tsarki yana da 'ya mace wadda kuke qi?. (22) Wannan rabo da kuka yi shi bisa son zuciyarku, rabo ne karkatacce. (23) Waxannan gumaka ba komai ba ne face zallar sunaye, da basa xauke da wata ma'ana, kuma basu da wani rabo a cikin siffofin allantaka, ku da iyayenku ne kuka sanya musu waxannan sunaye, Allah bai saukar da wani dalili a kansu ba. Kuma Mushirikai ba komai suke bi ba a cikin aqidarsu face zato, da abin da zukatansu suke so, daga cikin abin da Shaixan ya qawata musu a zukatansu, kuma haqiqa shiriya ta zo musu daga Ubangijinsu, a bisa harshen Annabinsa (S.A.W), amma basu shiryu da ita ba. (24) Ko mutum yana da abin da yake buri ne na ceton gumaka a wurin Allah?. (25) A'a, ba zai samu abin da ya yi buri ba, domin lahira ta Allah ce kaxai, haka ma duniya, yana bada su ga wanda ya ga dama, kuma ya hana wanda ya ga dama. (26) Kuma da yawa Mala'ikun da suke cikin sammai, cetonsu ba zai amfanar da komai ba, da ace zasu so su yi ceton a kan kansu, sai dai bayan Allah ya bada izinin yin ceton, ga wanda ya so, kuma ya yarda da wanda za a ceta xin, sai dai Allah ba zai bada izini ga wanda ya sanya masa abonkin tarayya ba a kan ya yi ceto, kuma ba zai yarda da wanda za a ceta ba matuqar yana bautawa wanin Allah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Cikar ladabin Annabi (S.A.W) ta yadda ganinsa bai kauce ya kalli wani wuri a saman bakwai ba. 2 - Wautar hankalin Mushirikai, ta fuskar bautarsu ga abin da baya cutarwa, baya amfanarwa, kuma suka danganawa Allah abin da basa so, su kuma suka zavi abin da suke so. 3 - Ceto baya tabbata sai da sharaxai guda biyu: samun izini ga mai ceto, da kuma yarda da wanda za a ceta.**

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡأٓخِرَةِ لَيُسَمُّونَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ تَسۡمِيَةَ ٱلۡأُنثَىٰ ٢٧
وَمَا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٍۖ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّۖ وَإِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغۡنِي مِنَ
ٱلۡحَقِّ شَيۡـٔٗا ٢٨ فَأَعۡرِضۡ عَن مَّن تَوَلَّىٰ عَن ذِكۡرِنَا وَلَمۡ يُرِدۡ إِلَّا ٱلۡحَيَوٰةَ
ٱلدُّنۡيَا ٢٩ ذَٰلِكَ مَبۡلَغُهُم مِّنَ ٱلۡعِلۡمِۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعۡلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن
سَبِيلِهِۦ وَهُوَ أَعۡلَمُ بِمَنِ ٱهۡتَدَىٰ ٣٠ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي
ٱلۡأَرۡضِ لِيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ بِمَا عَمِلُواْ وَيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ
بِٱلۡحُسۡنَى ٣١ ٱلَّذِينَ يَجۡتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلۡإِثۡمِ وَٱلۡفَوَٰحِشَ إِلَّا ٱللَّمَمَۚ
إِنَّ رَبَّكَ وَٰسِعُ ٱلۡمَغۡفِرَةِۚ هُوَ أَعۡلَمُ بِكُمۡ إِذۡ أَنشَأَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ
وَإِذۡ أَنتُمۡ أَجِنَّةٞ فِي بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡۖ فَلَا تُزَكُّوٓاْ أَنفُسَكُمۡۖ هُوَ أَعۡلَمُ
بِمَنِ ٱتَّقَىٰٓ ٣٢ أَفَرَءَيۡتَ ٱلَّذِي تَوَلَّىٰ ٣٣ وَأَعۡطَىٰ قَلِيلٗا وَأَكۡدَىٰٓ
٣٤ أَعِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلۡغَيۡبِ فَهُوَ يَرَىٰٓ ٣٥ أَمۡ لَمۡ يُنَبَّأۡ بِمَا فِي صُحُفِ
مُوسَىٰ ٣٦ وَإِبۡرَٰهِيمَ ٱلَّذِي وَفَّىٰٓ ٣٧ أَلَّا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰ
٣٨ وَأَن لَّيۡسَ لِلۡإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ٣٩ وَأَنَّ سَعۡيَهُۥ سَوۡفَ يُرَىٰ
٤٠ ثُمَّ يُجۡزَىٰهُ ٱلۡجَزَآءَ ٱلۡأَوۡفَىٰ ٤١ وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلۡمُنتَهَىٰ ٤٢
وَأَنَّهُۥ هُوَ أَضۡحَكَ وَأَبۡكَىٰ ٤٣ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَمَاتَ وَأَحۡيَا ٤٤



**(27) Haqiqa waxanda basa yin imani da tashi bayan mutuwa a gidan Lahira, tabbas suna kiran Mala'iku a matsayin jinsin mata, saboda sun qudurce cewa su Mala'iku 'ya'yan Allah ne mata, Allah ya xaukaka a kan maganar su xaukaka mai girma. (28) Basu da wani ilimi da suka dogara da shi a kan kiran Mala'iku da jinsin mata, ba abin da suke bi a cikin haka sai zato da kirdado, zato kuwa baya wadatar da komai a kan gaskiya, ballantana ya tsaya a matsayinta. (29) Ya kai wannan Manzo, ka kawar da kanka daga wanda ya bada baya daga ambaton Allah, ya zama bai damu da shi ba, ba abin da ya dame shi sai rayuwar duniya, don haka shi baya yin wani aiki saboda lahirarsa, domin bai yi imani da ita ba.**
**(30) Wancan abin da mushirikan nan suke faxa, na kiran Mala'iku da jinsin mata, shi ne iyakar saninsu, saboda su jahilai ne, har yanzu basu samu yaqini ba. Haqiqa Ubangijinka shi ne ya fi sanin wanda ya kaucewa hanyar gaskiya, kuma shi ne ya fi sanin wanda ya shiriya ga hanyarsa, babu abin da yake vuyar masa a cikin hakan.**
**(31) Na Allah ne shi kaxai abin da yake cikin sammai, kuma shi yake da abin da yake cikin qasa, mallakinsa ne, halittarsa ne, kuma tsarinsa ne, don ya sakawa waxanda suka munana aiki a duniya da irin abin da ya cancance su na azaba, kuma yana sakawa Muminai waxanda suka kyautata aikinsu da Aljannah. (32) Waxanda suke nisantar manyan laifuka da munanan savo, sai 'yan qananan zunubai, su kuma ana gafarta su ta hanyar barin manyan zunubai da yawaita xa'a ga Allah. Haqiqa Ubangijinka mai yalwar gafara ne – Ya kai wannan Manzo - yana gafarta zunuban bayinsa a duk lokacin da suka tuba, kuma shi Allah mai tsarki shi ne mafi sanin halayenku da lamuranku, yayin da ya halicci babanku Annabi Adamu daga turvaya, da lokacin da kuka kasance a cikin mahaifar iyayenku mata, ana halittar ku, halitta bayan halitta, babu wani abin da yake vuya a gare shi daga cikin haka, don haka kada ku yabi kanku da tsoron Allah, Allah Maxaukakin sarki shi ne mafi sanin wanda ya fi tsoronsa, ta hanyar kamanta umarninsa da kuma nisantar haninsa.**
**(33) Shin baka ga munin halin wanda ya bawa Musulunci baya ba, bayan ya kusance shi?.**
**(34) Kuma ya bayar da kaxan daga cikin dukiyarsa, sannan ya hana, saboda rowa ta zamar masa xabi'a, amma duk da haka yana tsarkake kansa.**
**(35) Shin yana da ilimin gaibu ne, wanda yake ganin komai da shi, kuma yake bada labari da shi?.**
**(36) Ko dai kawai qage yake yi wa Allah? Shin ba a bawa wannan mai qirqirar zancen ga Allah labarin abubuwan da suke cikin takardun farko ba, waxanda Allah ya saukarwa Annabi Musa?.**
**(37) Da labarin takardun da aka saukar wa Annabi Ibrahim, wanda ya sauke dukkan nauyin da Allah ya xora masa, kuma ya cika shi. (38) Cewa: wani mutum baya xaukan laifin wani.**
**(39) Kuma cewa mutum bashi da wani lada sai ladan aikin da ya aikata da kansa.**
**(40) Kuma haqiqa zai ga aikinsa ranar alqiyama a bayyane.**
**(41) Sannan kuma a bashi sakamakon aikinsa cikakke, ba tare da an rage masa komai ba.**
**(42) Ya kai wannan Manzo, kuma haqiqa makomar bayi, bayan mutuwarsu, tana ga Ubangijinka ne.**
**(43) Kuma shi ne yake farantawa wanda ya ga dama, ya sa shi dariya, kuma ya baqantawa wanda ya ga dama, ya sa shi kuka.**
**(44) Kuma shi ne ya kashe rayayyu a duniya, kuma ya raya matattu a ranar tashin alqiyama.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Zunubai sun kasu gida biyu: Manya da qanana. 2 - Haxarin yi wa Allah qarya ba tare da wani ilimi ba. 3 - Hana tsarkake kai.**

وَأَنَّهُۥ خَلَقَ ٱلزَّوْجَيْنِ ٱلذَّكَرَ وَٱلْأُنثَىٰ ٤٥ مِن نُّطْفَةٍ إِذَا تُمْنَىٰ
٤٦ وَأَنَّ عَلَيْهِ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُخْرَىٰ ٤٧ وَأَنَّهُۥ هُوَ أَغْنَىٰ وَأَقْنَىٰ ٤٨ وَأَنَّهُۥ
هُوَ رَبُّ ٱلشِّعْرَىٰ ٤٩ وَأَنَّهُۥٓ أَهْلَكَ عَادًا ٱلْأُولَىٰ ٥٠ وَثَمُودَاْ فَمَآ
أَبْقَىٰ ٥١ وَقَوْمَ نُوحٍ مِّن قَبْلُ إِنَّهُمْ كَانُواْ هُمْ أَظْلَمَ وَأَطْغَىٰ
٥٢ وَٱلْمُؤْتَفِكَةَ أَهْوَىٰ ٥٣ فَغَشَّىٰهَا مَا غَشَّىٰ ٥٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكَ تَتَمَارَىٰ ٥٥ هَٰذَا نَذِيرٌ مِّنَ ٱلنُّذُرِ ٱلْأُولَىٰٓ ٥٦ أَزِفَتِ ٱلْءَازِفَةُ
٥٧ لَيْسَ لَهَا مِن دُونِ ٱللَّهِ كَاشِفَةٌ ٥٨ أَفَمِنْ هَٰذَا ٱلْحَدِيثِ
تَعْجَبُونَ ٥٩ وَتَضْحَكُونَ وَلَا تَبْكُونَ ٦٠ وَأَنتُمْ سَٰمِدُونَ
٦١ فَٱسْجُدُواْ لِلَّهِ وَٱعْبُدُواْ ۩ ٦٢ سَجْدَة

آياتها ٥٥ سُورَةُ القَمَرِ ترتيبها ٥٤

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱقْتَرَبَتِ ٱلسَّاعَةُ وَٱنشَقَّ ٱلْقَمَرُ ١ وَإِن يَرَوْاْ ءَايَةً يُعْرِضُواْ وَيَقُولُواْ
سِحْرٌ مُّسْتَمِرٌّ ٢ وَكَذَّبُواْ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهْوَآءَهُمْ وَكُلُّ أَمْرٍ مُّسْتَقِرٌّ ٣
وَلَقَدْ جَآءَهُم مِّنَ ٱلْأَنۢبَآءِ مَا فِيهِ مُزْدَجَرٌ ٤ حِكْمَةٌۢ بَٰلِغَةٌ فَمَا تُغْنِ
ٱلنُّذُرُ ٥ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ يَوْمَ يَدْعُ ٱلدَّاعِ إِلَىٰ شَيْءٍ نُّكُرٍ ٦



**(45) Kuma shi ne wanda ya halicci jinsi biyu, namiji da mace. (46) Daga xigon maniyi, a lokacin da aka sanya shi a cikin mahaifa. (47) Kuma dawo da halittarsu bayan sun mutu domin tashin alqiyama a kansa yake. (48) Kuma shi ne wanda ya wadata wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ta hanyar mallaka masa dukiya, kuma ya bada dukiyar da daga cikinta ne mutane suke samun abin da suke tanada su ajiye. (49) Kuma shi ne Ubangijin tauraron Shi'ira, wato tauraron da wasu mushirikai suke bautawa tare da Allah.**

**(50) Kuma tabbas shi ne wanda ya halakar da Adawan farko, su ne mutanen Annabi Hudu a lokacin da suka zarce a kan kafirci. (51) Kuma ya halakar da Samudawa, mutanen Annabi Salihu, bai bar kowa daga cikinsu ba. (52) Kuma ya halakar da mutanen Annabi Nuhu, kafin zuwan Adawa da Samudawa. Tabbas mutanen Annabi Nuhu sun kasance mafi tsananin zalunci da shisshigi fiye da Adawa da Samudawa, saboda Annabi Nuhu ya zauna a cikinsu shekara dubu babu hamsin yana kiransu zuwa kaxaita Allah, amma basu amsa masa ba. (53) Alqaryar mutanen Annabi Luxu Allah ya xaga ta sama, sannan ya juya ta, ya kifar da ita zuwa qasa. (54) Ya rufe ta, abin da ya same ta na duwatsu ya same ta, bayan an xaga ta zuwa sama an kifar da ita a qasa.**

**(55) To da wace aya ce a cikin ayoyin Ubangijinka, waxanda suke nuna ikonsa kake yin jayayya ya kai xan adam, kuma ka kasa wa'azantuwa?.**

**(56) Wannan Manzo da aka aiko muku shi, yana daga cikin jinsin Manzannin farko ne da aka aiko.**

**(57) Tashin alqiyama ya kusa. (58) Kuma babu wani abu da zai kawar da tashin alqiyamar idan ya zo, kuma babu wanda ya isa ya gano yaushe ne za a yi shi, sai dai Allah kaxai. (59) Shin yanzu wannan Alqur'anin da ake karanta muku kuke yin mamakin kasancewar sa daga wurin Allah?. (60) Kuke yin dariya domin izgilanci da shi, ba kwa yin kuka yayin jin wa'azinsa? (61) Kuma kuna masu rafkana daga barinsa, baku damu da shi ba?. (62) To ku yi sujjada ga Allah shi kaxai, kuma ku tsarkake bauta a gare shi.**

# Suratul Qamar

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Tunatarwa ta hanyar kawo ayoyi da gargaxi, da bayanin makomar masu qaryata waxannan ayoyin, don haka faxin Allah: (Haqiqa mun sauwaqe Alqur'ani domin tunatarwa, to shin akwai masu tunawar) ya maimaita.**

**Tafsir:** **(1) Zuwan tashin alqiyama ya kusa. Wata ya tsage a zamanin Annabi (S.A.W). don haka wannan tsagewar aya ce da ake gani dake tabbatar da Manzancin Manzon Allah (S.A.W). (2) Idan mushirikai suka ga wani dalili da hujja a kan gaskiyar Manzon Allah (S.A.W) sai su bada baya ga karvarsa, su ce: "Abin da muka gani na hujjoji tsafi ne vatacce". (3) Suka qaryata abin da ya zo musu na gaskiya, suka biyewa son zukatansu cikin qaryatawa, to dukkan wani lamari na alheri ko sharri tabbas zai afku a ranar alqiyama ga wanda ya cancance shi. (4) Haqiqa labarun al'ummun da Allah ya halakar da su saboda zaluncinsu da kafircinsu ya zo wa al'ummarka, wanda wannan labarun kawai sun isa su tsawatar da su a kan zaluncinsu da kafircinsu. (5) Kuma abin da ya zo musu hikima ce cikakkiya, domin hujja ta tsaya a kansu, sai dai gargaxi baya amfanar mutanen da basa yin imani da Allah, koda ranar lahira. (6) To idan basu shiryu ba, ka rabu da su kawai - Ya kai wannan Manzo - ka basu baya, kana mai sauraron ranar da Mala'ika, wanda aka wakilta zai yi busa a cikin qaho, zai yi kira zuwa ga lamari mai ban tsoro, wanda kaf halitta basu san irinsa ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Rashin tasirantuwa da Alqur'ani alama ce dake nuna haxarin da mutum yake ciki. 2 - Haxarin bin son zuciya ga mutum, a duniya da lahira. 3 - Rashin wa'azantuwa da halakar da al'ummu siffa ce daga cikin siffofin kafirai.**

ثلاثة أرباع الحزب ٥٣

خُشَّعًا أَبۡصَٰرُهُمۡ يَخۡرُجُونَ مِنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ كَأَنَّهُمۡ جَرَادٞ مُّنتَشِرٞ ٧
مُّهۡطِعِينَ إِلَى ٱلدَّاعِۖ يَقُولُ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا يَوۡمٌ عَسِرٞ ٨ ۞ كَذَّبَتۡ
قَبۡلَهُمۡ قَوۡمُ نُوحٖ فَكَذَّبُواْ عَبۡدَنَا وَقَالُواْ مَجۡنُونٞ وَٱزۡدُجِرَ ٩ فَدَعَا
رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَغۡلُوبٞ فَٱنتَصِرۡ ١٠ فَفَتَحۡنَآ أَبۡوَٰبَ ٱلسَّمَآءِ بِمَآءٖ مُّنۡهَمِرٖ
١١ وَفَجَّرۡنَا ٱلۡأَرۡضَ عُيُونٗا فَٱلۡتَقَى ٱلۡمَآءُ عَلَىٰٓ أَمۡرٖ قَدۡ قُدِرَ ١٢
وَحَمَلۡنَٰهُ عَلَىٰ ذَاتِ أَلۡوَٰحٖ وَدُسُرٖ ١٣ تَجۡرِي بِأَعۡيُنِنَا جَزَآءٗ لِّمَن كَانَ
كُفِرَ ١٤ وَلَقَد تَّرَكۡنَٰهَآ ءَايَةٗ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ١٥ فَكَيۡفَ كَانَ
عَذَابِي وَنُذُرِ ١٦ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ١٧
كَذَّبَتۡ عَادٞ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ١٨ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا
صَرۡصَرٗا فِي يَوۡمِ نَحۡسٖ مُّسۡتَمِرّٖ ١٩ تَنزِعُ ٱلنَّاسَ كَأَنَّهُمۡ أَعۡجَازُ نَخۡلٖ
مُّنقَعِرٖ ٢٠ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ٢١ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ
لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ٢٢ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِٱلنُّذُرِ ٢٣ فَقَالُوٓاْ أَبَشَرٗا
مِّنَّا وَٰحِدٗا نَّتَّبِعُهُۥٓ إِنَّآ إِذٗا لَّفِي ضَلَٰلٖ وَسُعُرٍ ٢٤ أَءُلۡقِيَ ٱلذِّكۡرُ عَلَيۡهِ
مِنۢ بَيۡنِنَا بَلۡ هُوَ كَذَّابٌ أَشِرٞ ٢٥ سَيَعۡلَمُونَ غَدٗا مَّنِ ٱلۡكَذَّابُ ٱلۡأَشِرُ
٢٦ إِنَّا مُرۡسِلُواْ ٱلنَّاقَةِ فِتۡنَةٗ لَّهُمۡ فَٱرۡتَقِبۡهُمۡ وَٱصۡطَبِرۡ ٢٧



**(7) Idanuwansu suna cikin qasqanci, suna fitowa daga qaburbura kamar farin da suka watse, yayin da suke tafiya zuwa wurin hisabi. (8) Suna yin gaggawa zuwa ga mai kira zuwa ga wannan wuri. Kafirai suna cewa: “Wannan rana, rana ce mai wahala, saboda abin da yake cikinta na tsanani da firgici”. (9) Mutanen Annabi Nuhu sun qaryata bawanmu Nuhu, tun gabanin waxannan masu qaryata da’awarka su qaryata ka - Ya kai wannan Manzo - lokacin da muka aika shi zuwa gare su, suka ce: “Mahaukaci ne” kuma suka kyare shi da dukkan cin zarafi da zagi da tsoratarwa, idan har bai daina kiransu ba. (10) Sai Annabi Nuhu ya kira Ubangijinsa yana mai cewa: “Haqiqa mutanena sun rinjaye ni, kuma basu amsa kirana ba, ka taimake ni a kansu ta hanyar saukar musu da uquba”. (11) Sai muka buxe qofofin sama, suna kwararo da ruwa mai qarfi mai tunkuxar juna, wani na bin wani”. (12) Kuma muka vuxe qasa, ta zama idanun ruwa, ruwa yana vulvulowa daga cikinta, sai ruwan da yake sauka daga sama ya haxu da ruwan da yake vulvulowa daga qasa, bisa ga umarnin Allah da ya tsara shi tun fil azal, sai kowa ya halaka sai wanda Allah ya tserar da shi. (13) Kuma muka xauki Annabi Nuhu a kan wani jirgin ruwa, wanda aka yi shi da alluna da qusoshi, muka tseratar da shi tare da mutanensa daga nutsewa a cikin ruwa. (14) Wannan jirgin ruwan ya gudu a cikin kumfar ruwa, wadda take haxewa da juna, a qarqashin ganin mu da kiyayewarmu, duk wannan domin taimakawa Annabi Nuhu, wanda mutanensa suka qaryata shi, kuma suka kafircewa abin da ya zo da shi daga wurin Allah. (15) Haqiqa mun bar wannan uqubar da muka yi musu ta zama izna da wa’azi, to shin akwai mai xaukan iznar da wannan abin da ya faru?. (16) Kuma yaya azabata ta kasance ga masu qaryatawa? kuma yaya gargaxina na halakar da su ya kasance?. (17) Haqiqa mun sauwaqe Alqur’ani domin tunawa da wa’azantuwa, to shin akwai mai yin izna da abin da yake cikinsa na izina da wa’azi?. (18) Adawa sun qaryata Annabinsu Hudu (A.S). Ku lura - Ya ku mutanen garin Makkah, yaya azabata ta kasance a kansu?! kuma yaya gargaxina ya kasance ga wasun su game da halakar da su?!. (19) Yayin da muka aika musu da iska mai sanyi, a wata rana da take cike da shu’umanci da sharri, kuma zata zarce tare da su har zuwa shigar su Jahannama.**

**(20) Tana tunvuke mutane daga qasa, ta yi wurgi da su, suna masu faxuwa da kawunan su, kai ka ce tushen bishiyoyin dabino ne da aka tunvuke su daga qasa. (21) Ya ku mutanen Makkah, ku lura mana yaya azabata ta kasance a kansu?! Kuma yaya gargaxina ya kasance ga wasun su ta hanyar azabtar da su?!. (22) Haqiqa mun sauwaqe Alqur’ani domin tunawa da wa’azantuwa, to shin akwai mai yin izna da abin da yake cikinsa na izina da wa’azi?. (23) Samudawa sun qaryata da abin da Annabinsu Salihu (A.S) ya yi musu gargaxi da shi.**

**(24) Suka ce cikin inkari da jayayya: “Shin zamu biyayya ga mutum guda xaya, daga cikin jinsinmu?. Haqiqa idan muka yi masa biyayya a cikin wannan yanayi, to mun yi nisa da gaskiya, mun kauce mata, kuma mun shiga wahala.**

**(25) Yanzu a ce an saukar masa da wahayi shi kaxai, an keve shi da shi daga cikinmu gaba xaya?. Ba haka abin yake ba, kawai dai shi maqaryaci ne mai girman kai.**

**(26) Da sannu ranar alqiyama zasu san wanene maqaryaci mai girman kai. Annabi Salihu ne ko su?.**

**(27) Tabbas mu, zamu fito da Taguwa daga cikin dutse, kuma zamu taso ta domin mu jarrabe su. Ka lura da abin da zasu aikata da abin da za a yi musu - Ya kai Annabi Salihu – kuma ka yi haquri a kan cutarwar da suke maka.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Halaccin yi wa kafirin da ya zarce a kan kafircinsa mummunar addu’a.**
**2 - Halakar da masu qaryatawa, da kuma tseratar da Muminai sunnace ta Allah.**
**3 - Sauwaqe Alqur’ani domin a kiyaye shi, kuma a tuna da ayoyinsa, sannan a wa’azantu da su.**

وَنَبِّئۡهُمۡ أَنَّ ٱلۡمَآءَ قِسۡمَةُۢ بَيۡنَهُمۡۖ كُلُّ شِرۡبٖ مُّحۡتَضَرٞ ٢٨ فَنَادَوۡاْ صَاحِبَهُمۡ
فَتَعَاطَىٰ فَعَقَرَ ٢٩ فَكَيۡفَ كَانَ عَذَابِي وَنُذُرِ ٣٠ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ
صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ فَكَانُواْ كَهَشِيمِ ٱلۡمُحۡتَظِرِ ٣١ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ
لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ٣٢ كَذَّبَتۡ قَوۡمُ لُوطِۭ بِٱلنُّذُرِ ٣٣ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا
عَلَيۡهِمۡ حَاصِبًا إِلَّآ ءَالَ لُوطٖۖ نَّجَّيۡنَٰهُم بِسَحَرٖ ٣٤ نِّعۡمَةٗ مِّنۡ عِندِنَاۚ
كَذَٰلِكَ نَجۡزِي مَن شَكَرَ ٣٥ وَلَقَدۡ أَنذَرَهُم بَطۡشَتَنَا فَتَمَارَوۡاْ بِٱلنُّذُرِ
٣٦ وَلَقَدۡ رَٰوَدُوهُ عَن ضَيۡفِهِۦ فَطَمَسۡنَآ أَعۡيُنَهُمۡ فَذُوقُواْ عَذَابِي
وَنُذُرِ ٣٧ وَلَقَدۡ صَبَّحَهُم بُكۡرَةً عَذَابٞ مُّسۡتَقِرّٞ ٣٨ فَذُوقُواْ
عَذَابِي وَنُذُرِ ٣٩ وَلَقَدۡ يَسَّرۡنَا ٱلۡقُرۡءَانَ لِلذِّكۡرِ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ٤٠
وَلَقَدۡ جَآءَ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ ٱلنُّذُرُ ٤١ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا كُلِّهَا فَأَخَذۡنَٰهُمۡ
أَخۡذَ عَزِيزٖ مُّقۡتَدِرٍ ٤٢ أَكُفَّارُكُمۡ خَيۡرٞ مِّنۡ أُوْلَٰٓئِكُمۡ أَمۡ لَكُم بَرَآءَةٞ
فِي ٱلزُّبُرِ ٤٣ أَمۡ يَقُولُونَ نَحۡنُ جَمِيعٞ مُّنتَصِرٞ ٤٤ سَيُهۡزَمُ ٱلۡجَمۡعُ
وَيُوَلُّونَ ٱلدُّبُرَ ٤٥ بَلِ ٱلسَّاعَةُ مَوۡعِدُهُمۡ وَٱلسَّاعَةُ أَدۡهَىٰ وَأَمَرُّ ٤٦
إِنَّ ٱلۡمُجۡرِمِينَ فِي ضَلَٰلٖ وَسُعُرٖ ٤٧ يَوۡمَ يُسۡحَبُونَ فِي ٱلنَّارِ عَلَىٰ
وُجُوهِهِمۡ ذُوقُواْ مَسَّ سَقَرَ ٤٨ إِنَّا كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَٰهُ بِقَدَرٖ ٤٩



**(28) Kuma ka basu labari cewa: ruwan rijiyarsu abin rabawa ne tsakaninsu da taguwa, rana xaya tata, rana xaya ta su, kuma kowa shi kaxai zai sha rabonsa a ranarsa. (29) Sai suka kirawo xan uwansu domin ya kashe taguwar, ya xauki takobi ya kashe ta, yana mai zartar da umarnin mutanensa. (30) Ya ku mutanen Makkah, ku lura mana yaya azabata ta kasance a kansu?! Kuma yaya gargaxina ya kasance ga wasun su ta hanyar azabtar da su?!. (31) Haqiqa mun aika musu tsawa guda xaya ta halakar da su, sai suka kasance kamar busasshiyar bishiyar da mai kiwo yake samar wa dabbobinsa da ya xaure. (32) Haqiqa mun sauwaqe Alqur'ani domin tunawa da wa'azantuwa, to shin akwai mai yin izna da abin da yake cikinsa na izina da wa'azi?. (33) Mutanen Annabi Luxu sun qaryata gargaxin da Manzonsa Luxu (A.S) ya yi musu. (34) Haqiqa mun aika musu da iska, tana jifansu da duwatsu, amma banda mabiya Annabi Luxu, su azaba bata same su ba, haqiqa mun tseratar da su daga gare ta, domin cikin dare ya fita da su kafin azabar ta afko a qarshen dare. (35) Mun tseratar da su daga azabar ne domin yi musu ni'ima daga gare mu, kuma irin wannan sakayyar da muka yi wa Annabi Luxu, haka muke sakawa duk wanda ya godewa ni'imar Allah. (36) Haqiqa Annabi Luxu ya tsoratar da su azabar mu, amma sai suka rinqa yin jayayya da wannana tsoratarwa tasa, kuma suka qaryata shi. (37) Kuma mutanen Annabi Luxu sun nemi ya bar su da waxannan baqin nasa daga cikin Mala'iku, don su aikata alfasha da su, sai muka rufe musu idanuwa basu gansu ba, kuma muka ce musu: "Ku xanxani azabata, da sakamakon gargaxina a gare ku".**
**(38) Haqiqa azaba ta afka musu a lokacin safiya, kuma zata ci gaba da samunsu har su isa lahira, sai kuma azabar lahira ta zo musu. (39) Kuma aka ce musu: "Ku xanxani azabata wadda na saukar muku da ita, kuma sakamakon gargaxin da Annabi Luxu ya yi muku". (40) Haqiqa mun sauwaqe Alqur'ani domin tunawa da wa'azantuwa, to shin akwai mai yin izna da abin da yake cikinsa na izina da wa'azi?. (41) Haqiqa gargaxin mu ya zo wa mutanen Fir'auna, a bisa harshen Annabi Musa da Haruna (A.S). (42) Sai suka qaryata hujjoji da dalilai da suka zo musu daga wurin mu, sai muka yi musu uquba a kan wannan qaryatawar da suka yi, uqubar Allah Mabuwayi wanda babu mai rinjayarsa, kuma mai ikon da babu abin da yake gajiyar da shi. (43) Ya ku mutanen Makkah, shin kafiranku sun fi waxancan kafiran da aka ambata a baya alheri ne: mutanen Annabi Nuhu, da Adawa, da Samudawa, da mutanen Annabi Luxu, da Fir'auna da mutanensa?. ko kuwa kuna da tabbacin kuvuta daga azabar Allah da littafan sama suka zo da ita ne?. (44) Kawai dai waxannan kafirai na garin Makkah suna cewa ne: "Mu masu cin nasara ne a kan duk wanda ya nufe mu da mummunan abu, kuma yake nufin raba kanmu?.**
**(45) Za a karya taron waxannan kafirai, su juya da baya a gaban muminai. Kuma hakan ya faru a ranar Badar**
**(46) Kuma haqiqa alqiyamar da suke qaryatawa da ita, ita ce ranar da za'a azabtar da su, kuma bala'in da yake cikinta yafi tsanani, da girma a kan abin da suka haxu da shi a duniya, a ranar yaqin Badar.**
**(47) Haqiqa masu Laifi da yin kafirci da Savon Allah, suna cikin vacewa daga gaskiya, da azaba da wahala.**
**(48) Ranar da za a ja su a cikin wuta a kan fuskokin su, kuma a ce da su, don wulaqantarwa : "Ku xanxani azabar wuta". (49) Tabbas mu, mun halicci komai a faxin duniya, bisa yadda muka riga muka tsara, kuma a kan sanin mu da yadda muka ga dama, kuma bisa abin da muka rubuta a cikin Lauhul Mahfuz.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Gamewar azaba ga wanda ya aikata laifi kai tsaye, da kuma wanda ya tallafa aka aikata. 2 - Godewa Allah a kan ni'imarsa sababi ne na kuvuta daga azaba. 3 - Labarin da Alqur'ani ya bayar na rugujewar mushirikai a ranar yaqin Badar, tun kafin faruwar abin, yana daga cikin bada labarin voyayyun abubuwa (Gaibu), wanda yake nuna gaskiyar Alqur'ani. 4 - Wajabcin yin imani da qaddara.**

وَمَآ أَمۡرُنَآ إِلَّا وَٰحِدَةٞ كَلَمۡحِۭ بِٱلۡبَصَرِ ٥٠ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَآ
أَشۡيَاعَكُمۡ فَهَلۡ مِن مُّدَّكِرٖ ٥١ وَكُلُّ شَيۡءٖ فَعَلُوهُ فِي ٱلزُّبُرِ
٥٢ وَكُلُّ صَغِيرٖ وَكَبِيرٖ مُّسۡتَطَرٌ ٥٣ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ
فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ٥٤ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۭ ٥٥

## سُورَةُ الرَّحۡمَٰن

آياتها ٧٨ — ترتيبها ٥٥

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلرَّحۡمَٰنُ ١ عَلَّمَ ٱلۡقُرۡءَانَ ٢ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ ٣ عَلَّمَهُ ٱلۡبَيَانَ ٤ الحِزۡب ٥٤
ٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُ بِحُسۡبَانٖ ٥ وَٱلنَّجۡمُ وَٱلشَّجَرُ يَسۡجُدَانِ ٦
وَٱلسَّمَآءَ رَفَعَهَا وَوَضَعَ ٱلۡمِيزَانَ ٧ أَلَّا تَطۡغَوۡاْ فِي ٱلۡمِيزَانِ ٨
وَأَقِيمُواْ ٱلۡوَزۡنَ بِٱلۡقِسۡطِ وَلَا تُخۡسِرُواْ ٱلۡمِيزَانَ ٩ وَٱلۡأَرۡضَ
وَضَعَهَا لِلۡأَنَامِ ١٠ فِيهَا فَٰكِهَةٞ وَٱلنَّخۡلُ ذَاتُ ٱلۡأَكۡمَامِ ١١
وَٱلۡحَبُّ ذُو ٱلۡعَصۡفِ وَٱلرَّيۡحَانُ ١٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
١٣ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِن صَلۡصَٰلٖ كَٱلۡفَخَّارِ ١٤ وَخَلَقَ ٱلۡجَآنَّ مِن
مَّارِجٖ مِّن نَّارٖ ١٥ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٦ رَبُّ
ٱلۡمَشۡرِقَيۡنِ وَرَبُّ ٱلۡمَغۡرِبَيۡنِ ١٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ١٨



**(50) Lamarinmu ba komai ba ne a yayin da muka yi nufin wani abu, face mu faxi kalma xaya, ita ce "Kasance" sai abin da muka yi nufin ya kasance cikin sauri kamar qiftawar ido . (51) Kuma haqiqa mun halakar da makamantan ku a cikin kafirci, daga Al'ummun da suka gabata, shin ko akwai wanda zai yi izna da hakan a cikinku, ya tsawatu daga kafircinsa? (52) Kowane aiki bayi suka aikata, to yana rubuce a cikin littafin Mala'ikun da suke kiyaye ayyukan bayi, babu abin da yake wuce su. (53) Dukkan wasu qananan ayyuka da qananan maganganu, haka ma manyansu, duk suna rubuce a cikin takardun ayyuka a Lauhul Mahfuz, za kuma a saka musu a kansu. (54) Tabbas masu jin tsoron Ubangijinsu, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, suna cikin Aljannatai, suna jin daxi a cikinsu, da kuma qoramu masu gudana. (55) Suna cikin wani wurin zama na gaskiya, wanda babu wargi ko savo a cikinsa, a wurin sarkin da ya mallaki dukkan komai, kuma mai ikon da babu abin da ya gagare shi, don haka kada ma ka tambayi irin abin da zasu samu a wurinsa na ni'ima madauwamiya.**

# Suratur Rahman

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Sanar da ni'imomin Allah masu girma, da alamomin rahamarsa bayyanannu a duniya da lahira, domin a kwaxaitar ga yin imani, da kuma tsawatarwa daga butulci.**

## Tafsir:

**(1) Mai rahama, ma'abocin rahama yalwatacciya. (2) Ya sanar da mutane Alqur'ani, ta hanyar sauwaqe hardace shi, da sauwaqe fahimtar ma'anoninsa. (3) Ya halicci mutum a daidaice, kuma ya kyautata surarsa. (4) Kuma ya sanar da shi yaya zai bayyana abin da yake cikin ransa, ta hanyar furtawa, ko kuma rubutawa. (5) Rana da wata duk ya qaddara su, suna tafiya a kan wani lissafi mai kyau, don mutane su san lissafin shekaru da abubuwan da ake lissafawa. (6) Tsirran da basu da itace da bishiyoyi duk suna yi wa Allah sujjada, suna masu miqa wuya, masu sallama masa. (7) Sama ya xagata a sama da qasa, ta zama rufi a gare ta, kuma ya tabbatar da adalci a bayan qasa, ya kuma umarci bayinsa da shi. (8) Ya tabbatar da adalci domin kada ku yi zalunci – Ya ku mutane - kuma ku yi ha'inci a cikin ma'auni da sikeli.**

**(9) Kuma ku tsayar da ma'auni a tsakaninku da adalci, kada ku tauye ma'auni ko sikeli yayin da kuke auna ko kuke aunawa waninku. (10) Qasa kuma ya sanyata shiryayya, domin halitta ta samu wurin zama a kanta.**

**(11) A cikinta akwai bishiyoyin da suke fito da 'ya'yan itatuwa na marmari, kuma da akwai bishiyoyin dabino, waxanda suke xauke da abubuwan da dabinon yake ciki. (12) A bayan qasa akwai shukar da take xauke da qwayar da ake sussukewa, kamar irinsu gero da alkama, kuma a kawai tsirran da kuke jin daxin qanshin su.**

**(13) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**

**(14) Allah ya halicci Annabi Adamu daga busasshen tavo, wanda yake yin amo, kamar dafaffen tavo.**

**(15) Kuma ya halicci uban aljanu daga harshen wuta zalla, wadda babu hayaqi a cikinta.**

**(16) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(17) Ubangijin mahudar rana da mafaxarta a lokuta guda biyu, lokacin sanyi da lokacin zafi.**

**(18) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Rubuta ayyuka qanana da manya a cikin takardun rubuta ayyuka. 2 - Farawar da Allah ya yi da ambaton ni'imarsa da alqur'ani, ya nuna matsayin Alqur'ani, da girman baiwar da ya yi wa bayi da shi. 3 - Matsayin adalci a cikin Musulunci. 4 - Ya wajaba mu san nimomin Allah, kuma mu gode masa, kada mu butulce masa, ko mu qaryata da su.**

مَرَجَ ٱلۡبَحۡرَيۡنِ يَلۡتَقِيَانِ ١٩ بَيۡنَهُمَا بَرۡزَخٞ لَّا يَبۡغِيَانِ ٢٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢١ يَخۡرُجُ مِنۡهُمَا ٱللُّؤۡلُؤُ وَٱلۡمَرۡجَانُ ٢٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢٣ وَلَهُ ٱلۡجَوَارِ ٱلۡمُنشَـَٔاتُ فِي ٱلۡبَحۡرِ كَٱلۡأَعۡلَٰمِ ٢٤
فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢٥ كُلُّ مَنۡ عَلَيۡهَا فَانٖ ٢٦ وَيَبۡقَىٰ وَجۡهُ
رَبِّكَ ذُو ٱلۡجَلَٰلِ وَٱلۡإِكۡرَامِ ٢٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٢٨
يَسۡـَٔلُهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ كُلَّ يَوۡمٍ هُوَ فِي شَأۡنٖ ٢٩ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٠ سَنَفۡرُغُ لَكُمۡ أَيُّهَ ٱلثَّقَلَانِ ٣١ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٢ يَٰمَعۡشَرَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِ إِنِ ٱسۡتَطَعۡتُمۡ
أَن تَنفُذُواْ مِنۡ أَقۡطَارِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ فَٱنفُذُواْۚ لَا تَنفُذُونَ
إِلَّا بِسُلۡطَٰنٖ ٣٣ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٤ يُرۡسَلُ عَلَيۡكُمَا
شُوَاظٞ مِّن نَّارٖ وَنُحَاسٞ فَلَا تَنتَصِرَانِ ٣٥ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٣٦ فَإِذَا ٱنشَقَّتِ ٱلسَّمَآءُ فَكَانَتۡ وَرۡدَةٗ كَٱلدِّهَانِ
٣٧ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٣٨ فَيَوۡمَئِذٖ لَّا يُسۡـَٔلُ عَن
ذَنۢبِهِۦٓ إِنسٞ وَلَا جَآنّٞ ٣٩ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٠
يُعۡرَفُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ بِسِيمَٰهُمۡ فَيُؤۡخَذُ بِٱلنَّوَٰصِي وَٱلۡأَقۡدَامِ ٤١



**(19) Allah ya haxa teku guda biyu a wuri xaya, mai gishiri da mai daxi, suna haxuwa kamar yadda ake gani a ido. (20) Amma a tsakaninsu akwai shamaki da yake hana kowane daga cikinsu ya yi rinjayi a kan xayan, don haka mai daxi yana nan yadda yake, haka ma mai gishiri yana nan yadda yake. (21) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (22) Manya manyan kayan ado da qanana suna fita daga dukkan waxannan tekunan guda biyu. (23) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (24) Allah ne kaxai yake sarrafa jiragen ruwa masu gudana a cikin tekuna, kai ka ce manya manyan duwatsu ne. (25) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (26) Duk wanda yake doron qasa daga cikin halittu halakakke ne babu makawa. (27) Amma fuskar Ubangijinka (Wato zatinsa) zata yi saura, ma'abocin girma da kyautatawa, da baiwa ga bayinsa, rasuwa bata samunsa. (28) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?! (29) Waxanda suke cikin sammai daga cikin Mala'iku da waxanda suke bayan qasa daga aljanu da mutane, suna tambayarsa buqatunsu. Kowace rana yana cikin wani sha'ani daga sha'anin bayinsa, na daga rayawa, da kashewa, da azurtawa, da sauransu.**
**(30) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (31) Zamu bar komai don yi muku hisabi - Ya ku mutane da aljanu – sai mu sakawa kowa da abin da ya kamace shi na lada ko uquba. (32) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?! (33) Allah zai ce ranar alqiyama, idan ya tara aljanu da mutane a wuri guda: "Ya ku taron aljanu da mutune, idan zaku iya samar wa kanku mafita, daga wani vangare da vangarorin sammai da qassai, to ku samar wa kanku mana, amma ba zaku tava iyawa ba sai da qarfi da hujja, amma ta yaya zaku iya hakan?. (34) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**
**(35) Ya ku mutune da aljanu, ana turo muku harshen wuta, wanda ba shi da gaurayen hayaqi a cikinsa, da kuma hayaqi wanda babu harshen wuta a cikinsa, kuma ba zaku iya kare kanku daga hakan ba.**
**(36) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**
**(37) Idan sama ta kekkece domin saukar Mala'iku daga cikinta, sai ta kasance jawur kamar wani mai wajen hasken launinsa. (38) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**
**(39) A cikin wannan rana mai girma, ba za a tambayi mutum da aljan laifukansu ba, saboda Allah ya riga ya san ayyukansu. (40) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**
**(41) Ana gane masu laifi a ranar alqiyama da alamominsu, shi ne baqin fuskarsu, da jan idanunsu, Kuma sai a haxa makwarkwaxar su da digadigan su, a wurga su a cikin wutar Jahannama.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Haxa tsakanin teku mai gishiri da mai daxi, ba tare da sun cuxanya da juna ba, yana daga cikin ikon Allah. 2 - Tabbatar da qarewa ga dukkan halitta, da tabbatar da wanzuwa ga Allah shi kaxai, kwaxaitarwa ga bayi a kan su rataya da Allah wanda yake wanzuwa, kada su dogara a kan waninsa. 3 - Tabbatar da siffar fuska ga Allah, bisa yadda ta dace da shi, ba tare da kamantawa ko misaltawa ba. 4 - Yi wa kafiri azaba kala-kala.

فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٢ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِي يُكَذِّبُ بِهَا
ٱلْمُجْرِمُونَ ٤٣ يَطُوفُونَ بَيْنَهَا وَبَيْنَ حَمِيمٍ ءَانٍ ٤٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ
رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٥ وَلِمَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ ٤٦ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٤٧ ذَوَاتَآ أَفْنَانٍ ٤٨ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٤٩ فِيهِمَا عَيْنَانِ تَجْرِيَانِ ٥٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٥١ فِيهِمَا مِن كُلِّ فَٰكِهَةٍ زَوْجَانِ ٥٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٥٣ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ فُرُشٍۭ بَطَآئِنُهَا مِنْ إِسْتَبْرَقٍ ۚ وَجَنَى ٱلْجَنَّتَيْنِ دَانٍ
٥٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٥٥ فِيهِنَّ قَٰصِرَٰتُ ٱلطَّرْفِ
لَمْ يَطْمِثْهُنَّ إِنسٌ قَبْلَهُمْ وَلَا جَآنٌّ ٥٦ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٥٧ كَأَنَّهُنَّ ٱلْيَاقُوتُ وَٱلْمَرْجَانُ ٥٨ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٥٩ هَلْ جَزَآءُ ٱلْإِحْسَٰنِ إِلَّا ٱلْإِحْسَٰنُ ٦٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٦١ وَمِن دُونِهِمَا جَنَّتَانِ ٦٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٦٣ مُدْهَآمَّتَانِ ٦٤ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٦٥ فِيهِمَا عَيْنَانِ نَضَّاخَتَانِ ٦٦ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٦٧
فِيهِمَا فَٰكِهَةٌ وَنَخْلٌ وَرُمَّانٌ ٦٨ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٦٩



**(42) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (43) Kuma za a ce da su cikin zargi: "Wannan ita ce wutar Jahannama wadda masu laifi suka kasance suna qaryatawa da ita a duniya, to yanzu gata nan a gaban idonsu, yanzu baza su iya inkarinta ba. (44) Suna kai kawo a tsakaninta da tafasasshen ruwa, mai tsananin zafi.**

**(45) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (46) Wanda ya ji tsoron tsayuwa a gaban ubangijinsa a lahira, kuma ya yi imani, ya yi aiki nagari, to yana da Aljannatai guda biyu.**

**(47) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (48) Waxannan Aljannatai guda biyu, ma'abota rassa ne guda biyu masu girma, kuma kyawawa masu 'ya'yan itatuwa. (49) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!. (50) A cikin waxannan Aljannatai guda biyu akwai idanuwan ruwa da ruwa yake gudana daga cikinsu. (51) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?! (52) Kuma a cikinsu akwai duk wani kayan marmari, iri biyu biyu, wanda ake jin daxi da su. (53) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(54) 'Yan Aljanna suna kashingixe a kan wasu shimfixu, cikinsu alhariri ne mai kauri. Kuma abin da ake samu na 'ya'yan itatuwa da kayan marmari, a cikin waxannan Aljannatai guda biyu a kusa suke, ta yadda na zaune da na kwance, da na tsaye duk suna iya kai hannu su tsinka. (55) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(56) Kuma a cikinsu da akwai mataye waxanda suka taqaita ganinsu ga mazajensu kaxai, kuma wani mutum ko aljani kafin mazajensu, bai kawar musu da budurci ba. (57) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**

**(58) Su waxannan 'yan matan na Aljanna (Idan ka gan su) kai ka ce yaqutu ne da murjani (wajen kyau da haske).**

**(59) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(60) Mene ne sakamakon wanda ya kyautata wurin yi wa Ubangijinsu xa'a, face shi ma Allah ya kyautata sakamakonsa?!**

**(61) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(62) Kuma bayan waxannan Aljannatai guda biyu da aka ambata, akwai wasu guda biyun daban.**

**(63) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**

**(64) Sun yi kore shar.**

**(65) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!**

**(66) A cikin waxannan Aljannatai guda biyu akwai idanun ruwa guda biyu, masu tsananin kwararo da ruwa, wanda kwararar bata yankewa.**

**(67) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**(68) A cikin waxannan Aljannatai guda biyu akwai kayan marmari masu yawa, da dabino mai girma, da ruman.**

**(69) To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Muhimmancin tsoron Allah, da kuma halarto da firgicin tsayuwa a gabansa. 2 - Yabon matan gidan aljannah da kamewa, yana nuna muhimmancin wannan sifa ga mace. 3 - Sakamako yana kasancewa daga irin aikin da aka yi.**

**70 A cikin waxannan Aljannatai akwai mataye masu matuqar kyawun hali da kyan fuska.**
**71 To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**
**72 Matan Hurul aini ababen suturcewa a cikin tantuna, don kare su daga dukkan komai.**
**73 To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**
**74 Kuma babu wanda ya kusance su da kwanciya, daga cikin mutane ko aljanu, kafin mazajensu.**
**75 To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**
**76 'Yan aljanna suna kashingixe a kan wasu matasan kai da aka rufe su da korayen abubuwa, da kuma shimfixu masu kyau.**
**77 To waxanne daga cikin ni'imomin Ubangijinku masu yawa kuke qaryatawa - Ya ku taron mutane da aljanu?!.**
**78 Alherin sunan Ubangijinka, ma'abocin girma da kyautatawa, da baiwa ga bayinsa ya yawaita.**

## Suratul Waqi'a

An Saukar Da Ita A Makkah

### Daga Manufofin Surar:

**Tsoratarwa da ranar alqiyama ta qunsa, da tabbatar da faruwarta, da rabe raben mutane a wannan rana, da bayanin sakamakon kowanne daga cikinsu.**

فِيهِنَّ خَيۡرَٰتٌ حِسَانٞ ٧٠ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ
٧١ حُورٞ مَّقۡصُورَٰتٞ فِي ٱلۡخِيَامِ ٧٢ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا
تُكَذِّبَانِ ٧٣ لَمۡ يَطۡمِثۡهُنَّ إِنسٞ قَبۡلَهُمۡ وَلَا جَآنّٞ ٧٤ فَبِأَيِّ
ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٧٥ مُتَّكِـِٔينَ عَلَىٰ رَفۡرَفٍ خُضۡرٖ
وَعَبۡقَرِيٍّ حِسَانٖ ٧٦ فَبِأَيِّ ءَالَآءِ رَبِّكُمَا تُكَذِّبَانِ ٧٧
تَبَٰرَكَ ٱسۡمُ رَبِّكَ ذِي ٱلۡجَلَٰلِ وَٱلۡإِكۡرَامِ ٧٨

ترتيبها ٥٦ — سُورَةُ الوَاقِعَةِ — آياتها ٩٦

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ربع الحزب ٥٤ إِذَا وَقَعَتِ ٱلۡوَاقِعَةُ ١ لَيۡسَ لِوَقۡعَتِهَا كَاذِبَةٌ ٢ خَافِضَةٞ رَّافِعَةٌ
٣ إِذَا رُجَّتِ ٱلۡأَرۡضُ رَجّٗا ٤ وَبُسَّتِ ٱلۡجِبَالُ بَسّٗا ٥ فَكَانَتۡ
هَبَآءٗ مُّنۢبَثّٗا ٦ وَكُنتُمۡ أَزۡوَٰجٗا ثَلَٰثَةٗ ٧ فَأَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ
مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ ٨ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ مَآ أَصۡحَٰبُ
ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ ٩ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلسَّٰبِقُونَ ١٠ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ١١
فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ١٢ ثُلَّةٞ مِّنَ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٣ وَقَلِيلٞ مِّنَ ٱلۡأٓخِرِينَ
١٤ عَلَىٰ سُرُرٖ مَّوۡضُونَةٖ ١٥ مُّتَّكِـِٔينَ عَلَيۡهَا مُتَقَٰبِلِينَ ١٦



### Tafsir:

**1 Idan alqiyama ta tsaya, kuma babu makawa.**
**2 Ba za a samu wata rai da zata qaryata faruwarta ba, kamar yadda take qaryatawa da ita a duniya.**
**3 Alqiyama mai qasqantar da kafirai fajirai ce, ta hanyar shigar da su cikin wuta, kuma mai xaukaka Muminai masu tsoron Allah ne, ta hanyar shigar da su cikin Aljanna.**
**4 Idan aka motsa qasa, motsawa mai girma.**
**5 Kuma a tarwatsa duwatsu tarwatsawa.**
**6 Suka zama qura mai watsuwa a ko'ina, saboda wannan motsawar.**
**7 Zaku kasance kaso uku a wannan rana:**
**8 Ma'abota hannun dama, waxanda zasu karvi littafinsu da hannun damansu, babu wanda ya kai xaukakarsu da matsayinsa!. 9 Da ma'abota hannun hagu, waxanda zasu karvi littafinsu da hannun hagunsu, ba wanda ya kai su qasqanci da mummunan matsayi!. 10 Da kuma masu rigaya a cikin ayyukan alheri a duniya, haka ma a lahira su ne masu rigaya wajen shiga Aljannah.**
**11 Kuma waxannan su ne makusanta a wurin Allah.**
**12 A cikin Aljannar ni'ima, suna jin daxi da ni'ima kala - kala.**
**13 Jama'a ne masu yawa daga cikin wannan al'umma da al'ummun da suka wuce.**
**14 Kaxan ne daga cikin mutane a qarshen zamani suke zamowa waxanda suka tsere sa'a, kuma makusanta ga Allah maxaukakin sarki.**
**15 Suna kan gadaje da aka saqa su da zinare.**
**16 Suna kashingixe a kan waxannan gadaje, suna kallon juna da fuskokinsu, babu wanda yake kallon qeyar wani.**

### Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tuna ni'imomin Allah da ayoyinsa a koyaushe, yana sa bawa ya riqa girmama Allah da kyautata biyayya a gare shi. 2 - Qaryatawar kafirai zata yanke a lokacin da suka ga alqiyama da idanunsu.**
**3 - Matsayin 'yan aljanna yana bambanta, saboda bambantar ayyukansu.**

يَطُوفُ عَلَيۡهِمۡ وِلۡدَٰنٞ مُّخَلَّدُونَ ١٧ بِأَكۡوَابٖ وَأَبَارِيقَ وَكَأۡسٖ مِّن مَّعِينٖ
١٨ لَّا يُصَدَّعُونَ عَنۡهَا وَلَا يُنزِفُونَ ١٩ وَفَٰكِهَةٖ مِّمَّا يَتَخَيَّرُونَ
٢٠ وَلَحۡمِ طَيۡرٖ مِّمَّا يَشۡتَهُونَ ٢١ وَحُورٌ عِينٞ ٢٢ كَأَمۡثَٰلِ ٱللُّؤۡلُوِٕ
ٱلۡمَكۡنُونِ ٢٣ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٢٤ لَا يَسۡمَعُونَ فِيهَا لَغۡوٗا
وَلَا تَأۡثِيمًا ٢٥ إِلَّا قِيلٗا سَلَٰمٗا سَلَٰمٗا ٢٦ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡيَمِينِ مَآ أَصۡحَٰبُ
ٱلۡيَمِينِ ٢٧ فِي سِدۡرٖ مَّخۡضُودٖ ٢٨ وَطَلۡحٖ مَّنضُودٖ ٢٩ وَظِلّٖ مَّمۡدُودٖ
٣٠ وَمَآءٖ مَّسۡكُوبٖ ٣١ وَفَٰكِهَةٖ كَثِيرَةٖ ٣٢ لَّا مَقۡطُوعَةٖ وَلَا مَمۡنُوعَةٖ
٣٣ وَفُرُشٖ مَّرۡفُوعَةٍ ٣٤ إِنَّآ أَنشَأۡنَٰهُنَّ إِنشَآءٗ ٣٥ فَجَعَلۡنَٰهُنَّ أَبۡكَارًا
٣٦ عُرُبًا أَتۡرَابٗا ٣٧ لِّأَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٣٨ ثُلَّةٞ مِّنَ ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٩
وَثُلَّةٞ مِّنَ ٱلۡأٓخِرِينَ ٤٠ وَأَصۡحَٰبُ ٱلشِّمَالِ مَآ أَصۡحَٰبُ ٱلشِّمَالِ
٤١ فِي سَمُومٖ وَحَمِيمٖ ٤٢ وَظِلّٖ مِّن يَحۡمُومٖ ٤٣ لَّا بَارِدٖ
وَلَا كَرِيمٍ ٤٤ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَبۡلَ ذَٰلِكَ مُتۡرَفِينَ ٤٥ وَكَانُواْ
يُصِرُّونَ عَلَى ٱلۡحِنثِ ٱلۡعَظِيمِ ٤٦ وَكَانُواْ يَقُولُونَ أَئِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا
تُرَابٗا وَعِظَٰمًا أَءِنَّا لَمَبۡعُوثُونَ ٤٧ أَوَءَابَآؤُنَا ٱلۡأَوَّلُونَ ٤٨ قُلۡ إِنَّ
ٱلۡأَوَّلِينَ وَٱلۡأٓخِرِينَ ٤٩ لَمَجۡمُوعُونَ إِلَىٰ مِيقَٰتِ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ٥٠



**17 Wasu yara suna kewayawa su domin yi musu
hidima, basa tsufa, ko mutuwa. 18 Suna kewaya
su da wasu kofuna marasa mariqai, da kuma
masu mariqai, da mazubai na giya, wadda take
gudana a cikin gidan Aljanna, bata yankewa.
19 Ba kamar giyar duniya take ba, mai shanta
baya yin ciwon kai, kuma hankalinsa baya
gushewa. 20 Waxannan yaran suna kewaya su
da kayan marmari, waxanda suka zava.
21 Suna kewayawa da naman tsuntsaye, wanda
rai yake sha'awa. 22 Kuma a cikin Aljanna suna
da mataye masu yalwar idanu, saboda kyan su.
23 Kai kace lu'u-lu'u ne wanda yake cikin
qwanson sa. 24 Wannan duk sakamako ne da
aka yi musu a kan ayyuka nagari da suka kasance
suna aikatawa a duniya. 25 A cikin Aljanna basa
jin zancen banza, ko wani zance da wanda ya
yi shi zai samu zunubi. 26 Basa jin komai sai
sallamar Mala'iku a gare su, da sallamar sashensu
ga sashe. 27 Ma'abota dama, su waye ma'abota
dama? Matsayinsu da sha'aninsu ya xaukaka a
wurin Allah. 28 Suna qarqashin itaciyar magarya
maras qaya a jikinta. kuma maras cutarwa.
29 Da ayaba wadda take cunkushe da juna,
sashenta kan sashe. 30 Da inuwa shimfixaxxiya
mai tsawo, wadda bata gushewa.
31 Da ruwa mai gudana, maras tsayawa.
32 Ga kayan marmari masu yawa, baza su lissafu
ba.
33 Basa yanke musu har abada, don basu da wani
lokaci qayyadadde, kuma babu wani abu da zai
hana su samunsu a duk lokacin da suka ga dama.
34 Da shimfixu maxaukaka, da ake sanya su a kan gadaje.
35 Haqiqa mun halicci matan hurun Eni, waxanda aka ambata, irin halittar da ba a tava ganin irinta ba.
36 Muka sanya su masu budurci, babu wanda ya taba kusantar su kafin mazajensu.
37 Kuma mazajensu suna son su, sannan tsarekun juna ne a shekaru.
38 Mun halicce su ne ga ma'abota dama, waxanda za a yi dama da su domin nuna alamar samun rabautarsu da
kuma jin daxinsu.
39 Su wasu jama'a ce daga cikin al'ummun Annabawan da suka gabata.
40 Da kuma wasu jama'a daga cikin al'ummar Annabi Muhammad (S.A.W) kuma su ne al'ummar qarshe.
41 Ma'abota hagu, ko kasan su wane ne ma'abota hagu? Tir da munin halinsu, da mummunar makomar su.
42 Suna cikin iska mai tsananin zafi, da ruwa shi ma mai tsananin zafi.
43 Kuma a qarqashin inuwar wani hayaqi baqi qirin.
44 Iskar sa bata da daxi, kuma ba shi da kyan gani.
45 Haqiqa sun kasance gabanin su tsinci kansu a cikin wannan azabar, masu jin daxi ne a duniya, basu da wani
tunani sai na sha'awar su. 46 Kuma sun kasance masu taurin kai a kan kafircewa Allah, da bautar gumaka,
koma bayan Allah. 47 Kuma sun kasance suna musun tashi bayan mutuwa, suna cewa cikin izgili da nuna rashin
yiwuwar sa: "Yanzu idan muka mutu, muka zama turvaya, da qasusuwa ruvavvu, wai za a tashe mu bayan haka?!.
48 Yanzu za a tashi iyayenmu na farko, waxanda suka mutu gabaninmu?!.
49 Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxannan masu musun tashi bayan mutuwa, ka ce da su: "Tabbas mutanen
farko da mutanen qarshe.
50 Za a tara su a ranar alqiyama babu makawa, domin a yi musu hisabi da sakayya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Aiki nagari sababi ne na samun ni'ima a lahira. 2 - Holewa da jin daxi suna cikin abubuwan da suke jefa mutum
cikin savon Allah. 3 - Haxarin zarcewa a kan laifi.**

ثُمَّ إِنَّكُمْ أَيُّهَا ٱلضَّآلُّونَ ٱلْمُكَذِّبُونَ ٥١ لَأَكِلُونَ مِن شَجَرٍ مِّن زَقُّومٍ ٥٢
فَمَالِـُٔونَ مِنْهَا ٱلْبُطُونَ ٥٣ فَشَٰرِبُونَ عَلَيْهِ مِنَ ٱلْحَمِيمِ ٥٤ فَشَٰرِبُونَ
شُرْبَ ٱلْهِيمِ ٥٥ هَٰذَا نُزُلُهُمْ يَوْمَ ٱلدِّينِ ٥٦ نَحْنُ خَلَقْنَٰكُمْ فَلَوْلَا
تُصَدِّقُونَ ٥٧ أَفَرَءَيْتُم مَّا تُمْنُونَ ٥٨ ءَأَنتُمْ تَخْلُقُونَهُۥٓ أَمْ نَحْنُ
ٱلْخَٰلِقُونَ ٥٩ نَحْنُ قَدَّرْنَا بَيْنَكُمُ ٱلْمَوْتَ وَمَا نَحْنُ بِمَسْبُوقِينَ ٦٠
عَلَىٰٓ أَن نُّبَدِّلَ أَمْثَٰلَكُمْ وَنُنشِئَكُمْ فِى مَا لَا تَعْلَمُونَ ٦١ وَلَقَدْ
عَلِمْتُمُ ٱلنَّشْأَةَ ٱلْأُولَىٰ فَلَوْلَا تَذَكَّرُونَ ٦٢ أَفَرَءَيْتُم مَّا تَحْرُثُونَ
٦٣ ءَأَنتُمْ تَزْرَعُونَهُۥٓ أَمْ نَحْنُ ٱلزَّٰرِعُونَ ٦٤ لَوْ نَشَآءُ لَجَعَلْنَٰهُ
حُطَٰمًا فَظَلْتُمْ تَفَكَّهُونَ ٦٥ إِنَّا لَمُغْرَمُونَ ٦٦ بَلْ نَحْنُ
مَحْرُومُونَ ٦٧ أَفَرَءَيْتُمُ ٱلْمَآءَ ٱلَّذِى تَشْرَبُونَ ٦٨ ءَأَنتُمْ أَنزَلْتُمُوهُ
مِنَ ٱلْمُزْنِ أَمْ نَحْنُ ٱلْمُنزِلُونَ ٦٩ لَوْ نَشَآءُ جَعَلْنَٰهُ أُجَاجًا فَلَوْلَا
تَشْكُرُونَ ٧٠ أَفَرَءَيْتُمُ ٱلنَّارَ ٱلَّتِى تُورُونَ ٧١ ءَأَنتُمْ أَنشَأْتُمْ
شَجَرَتَهَآ أَمْ نَحْنُ ٱلْمُنشِـُٔونَ ٧٢ نَحْنُ جَعَلْنَٰهَا تَذْكِرَةً وَمَتَٰعًا
لِّلْمُقْوِينَ ٧٣ فَسَبِّحْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلْعَظِيمِ ٧٤ ۞ فَلَآ أُقْسِمُ نصف الحزب ٥٤
بِمَوَٰقِعِ ٱلنُّجُومِ ٧٥ وَإِنَّهُۥ لَقَسَمٌ لَّوْ تَعْلَمُونَ عَظِيمٌ ٧٦



**51 Sannan ku - masu qaryata tashi bayan mutuwa - vatattu ne ga tafarki madaidaici.**
**52 Tabbas ranar alqiyama sai kun ci daga 'ya'yan itatuwar Zaqqum, kuma shi ne mafi sharrin xan itace, mafi muni. 53 Kuma tabbas sai kun cika cikinku, wanda babu komai, daga wannan bishiya mai xaci. 54 Kuma zaku biye masa da shan tafasasshen ruwa mai tsananin zafi. 55 Zaku yawaita shan wannan ruwa, kamar yadda raqumi yake yawaita shan ruwa idan cutar (Huyam) ta kama shi. 56 Wannan abin da aka ambata na abinci mai xaci, da tafasasshen ruwa shi ne liyafar 'yan wuta, wadda za a tarbe su da ita ranar da sakamako. 57 Mu ne muka halicce ku - Ya ku masu qaryatawa - bayan da kun kasance babu, to me zai hana ku gamsu zamu iya dawo da ku a raye bayan kun mutu?!. 58 Ya ku mutane, shin baku ga abin da kuke sanyawa a cikin mahaifar matayen ku na maniyyi ba?!. 59 Shin ku ne kuke halittar wannan maniyyin, ko kuwa mu ne muka halicce shi?! 60 Mu ne muka qaddara mutuwa a tsakaninku, kowane xaya daga cikinku yana da ajali, da bai isa ya tsallake shi ba, ko kuma ya gaza shi, kuma mu ba masu gazawa ba ne.**
**61 Akan mu canza abin da kuke kai na halitta, ko na sura daga yadda kuka san shi, kuma mu fare ku a wata surar da halittar da ba ku san irinta ba.**
**62 Kuma haqiqa kun san yaya muka halicce ku da farko. to shin ba zaku xau izina da hakan ba, ku san cewa: wanda ya halicce ku da farko, mai cikakken iko ne a kan tashin ku bayan kun mutu?!. 63 Shin ba ku ga irin da kuke shukawa a bayan qasa ba?! 64 Ku ne kuke tsuro da wannan irin, ko kuwa mu ne muke tsiro da shi?!**
**65 Da mun ga damar sanya wannan shukar karmami, da mun sanya ta karmamin bayan ta kusa nuna, kuma ku zo kuna ta yin mamakin faruwar abin da ya same ta. 66 Kuna cewa: "Haqiqa an mana azaba da yin asarar abin da muka ciyar ga wannan shuka". 67 Kawai dai an haramta mana samun arziki ne.**
**68 Shin baku ga ruwan da kuke sha ba ne, yayin da kuke jin qishirwa?!**
**69 Ku ne kuka saukar da shi daga girgije daga sama, ko kuwa mu ne muka saukar da shi?!.**
**70 Da mun ga damar sanya wannan ruwa ya zamo mai tsananin zartsi, yadda ba za a amfanu da shi ba, wurin sha, ko shayarwa, da mun sanya shi mai tsananin zartsin, to ba zaku godewa Allah ba, a kan saukar muku da shi ruwan daxi, domin jin qai da rahama a gare ku?!**
**71 Shin ba ku ga wutar da kuke kunnawa ba domin amfanin kanku?!**
**72 Shin ku ne kuka farar da bishiyar da ake kunna daga gare ta, ko kuwa mu ne muka farar da ita, domin tausayawa a gare ku?!.**
**73 Mu ne muka sanya wannan wutar ta zamo tunatarwa a gare ku, tana tuna muku wutar lahira, kuma muka sanya ta ta zamo mai amfani ga matafiya a cikinku.**
**74 Ya kai wannan Manzo, ka tsarkake Ubangijinka mai girma, daga duk abin da bai dace da shi ba.**
**75 Allah ya rantse da wuraren taurari da inda suke.**
**76 Kuma tabbas rantsuwa da waxannan wurare - da kun san girmansa - tabbas abu ne mai girma, saboda abin da yake cikinsa na ayoyi da izna maras iyaka.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Abin da yin halitta ta farko yake nunawa na sauqin faruwar tashi bayan mutuwa abu ne da yake a bayyane.**
**2 - Saukar da ruwan sama, da fito da tsiro daga qasa, da samar da wutar da mutane ke amfana da ita, duk ni'imomi ne da ya kamata mutane su godewa Allah a kai, domin Allah yana da ikon qwace a duk lokacin da ya ga dama.**
**3 - Qudurce cewa taurari suna da tasiri wurin saukar da ruwan sama kafirci ne, kuma yana cikin al'adun jahiliyya.**

إِنَّهُۥ لَقُرۡءَانٞ كَرِيمٞ ٧٧ فِي كِتَٰبٖ مَّكۡنُونٖ ٧٨ لَّا يَمَسُّهُۥٓ إِلَّا
ٱلۡمُطَهَّرُونَ ٧٩ تَنزِيلٞ مِّن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٨٠ أَفَبِهَٰذَا ٱلۡحَدِيثِ
أَنتُم مُّدۡهِنُونَ ٨١ وَتَجۡعَلُونَ رِزۡقَكُمۡ أَنَّكُمۡ تُكَذِّبُونَ ٨٢ فَلَوۡلَآ
إِذَا بَلَغَتِ ٱلۡحُلۡقُومَ ٨٣ وَأَنتُمۡ حِينَئِذٖ تَنظُرُونَ ٨٤ وَنَحۡنُ أَقۡرَبُ
إِلَيۡهِ مِنكُمۡ وَلَٰكِن لَّا تُبۡصِرُونَ ٨٥ فَلَوۡلَآ إِن كُنتُمۡ غَيۡرَ مَدِينِينَ
٨٦ تَرۡجِعُونَهَآ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٨٧ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلۡمُقَرَّبِينَ
٨٨ فَرَوۡحٞ وَرَيۡحَانٞ وَجَنَّتُ نَعِيمٖ ٨٩ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ
ٱلۡيَمِينِ ٩٠ فَسَلَٰمٞ لَّكَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡيَمِينِ ٩١ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ
ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ٩٢ فَنُزُلٞ مِّنۡ حَمِيمٖ ٩٣ وَتَصۡلِيَةُ جَحِيمٍ
٩٤ إِنَّ هَٰذَا لَهُوَ حَقُّ ٱلۡيَقِينِ ٩٥ فَسَبِّحۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلۡعَظِيمِ ٩٦

ترتيبها ٥٧ — سُورَةُ الحَدِيدِ — آياتها ٢٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١ لَهُۥ مُلۡكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٢ هُوَ
ٱلۡأَوَّلُ وَٱلۡأٓخِرُ وَٱلظَّٰهِرُ وَٱلۡبَاطِنُۖ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ٣



**(77) Haqiqa Alqur'anin da ake karanta muku – Ya ku mutane – qur'ani ne mai girma, saboda abin da yake cikinsa na amfani mai girma. (78) Kuma yana cikin littafi abin kiyayewa daga ganin mutane, shi ne Lauhul mahfuz. (79) Babu wanda suke tava shi sai Mala'iku, waxanda aka tsarkake su daga zunubai da kuma aibu. (80) Kuma shi abin saukarwa ne daga Ubangijin halitta, ga Annabinsa Muhammad (S.A.W). (81) Ya ku Mushirikai, yanzu da wannan maganar ne kuke qaryatawa, kuma kuke qin gasgatawa?! (82) Kuma ku ke sanya godiyar ku ga Allah a kan arzikin da ya yi muku na ni'imomi, shi ne qaryatawa da shi, sai ku danganta saukar ruwan sama ga wani tauraro, ku ce: "An mana ruwa daga tauraro kaza, mun samu ruwa daga tauraro kaza?!". Yayin da ya ambaci wasu dalilai na yiwuwar tashi bayan mutuwa, sai kuma ya yi nufin ya nusar a akan ikonsa na dawo da halitta ta hanyar nuna gajiyawar bayi wajen tunkuxe mutuwa, domin duk wanda ya kashe, to mai iko ne wajen ya raya. (83) Ina ma yayin da rai ya zo maqoshi. (84) Alhali ku a wannan lokaci kuna kallon wanda zai mutun a gabanku. (85) Mu kuma da ikon mu, da ilimin mu, da Mala'ikun mu, mun fi ku kusa da mamacinku, amma sai dai ba kwa ganin waxannan Mala'iku. (86) To me ya hana idan har – kamar yadda kuke riyawa ne – cewa ba za a tashe ku ba, don a saka muku a kan ayyukanku. (87) Ku dawo da wannan rai, wadda take fita daga jikin mamacin ku, idan har da gaske kuke. Amma ba zaku iya ba. (88) Amma idan mamacin ya kasance daga cikin masu yin rige-rige zuwa ayyukan alheri. (89) To tabbas yana da hutun da babu gajiya a bayansa, da kuma arziki mai kyau, da jin qai, kuma zai samu Aljannah, wadda zai ni'imta a cikinta da abin da ransa take so. (90) (91) Amma idan mamacin ya kasance daga cikin ma'abota hannun dama, to su ma dai kada ka damu da sha'aninsu, domin suna da kuvuta da aminci. (92) Amma idan mamacin ya kasance daga cikin masu qaryatawa da abin da Manzo (S.A.W) ya zo da shi ne, kuma vatacce daga tafarki madaidaici. (93) To liyafarsa wadda za a tarbe shi da ita, ruwa ne tafasasshe, mai tsananin zafi. (94) Kuma ga quna a cikin wutar Jahimu. (95) Tabbas wannan labarin da muka baka - Ya kai wannan Manzo- shi ne sakankacewa na gaskiya (Yaqini) wadda babu kokwanto a cikinsa ko kaxan. (96) Don haka ka tsarkake sunan Ubangijinka mai girma, kuma ka girmama shi daga duk wata tawaya.**

# Suratul Hadid

An Saukar Da Ita A Madinah

**Daga Manufofin Surar:** **Bayanin yadda ake gina imani mai qarfi da tanadi na duniya, wanda suke zaburarwa wajen da'awa da jihadi, da kuvutar da zukata daga abubuwan da suke hana da'awa da jihadi, don haka kalmar ciyarwa da imani suka maimaita a cikin surar.**

**Tafsir:** **(1) Abin da yake cikin sammai da qassai na halittar Allah yana tsarkake shi, kuma shi ne Mabuwayi, wanda babu mai rinjayarsa, mai hikima cikin halittarsa da kuma tsarinsa. (2) Shi kaxai yake da mulkin sammai da qassai, yana raya wanda ya ga damar ya raya shi, ya kashe wanda ya ga damar ya kashe shi, kuma shi mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gagararsa. (3) Shi ne na farkon da babu wani kafinsa, kuma shi ne na qarshen da babu komai a bayan sa, shi ne mabayyanin da babu komai a saman sa, kuma shi ne a voyen da babu komai bayan sa, kuma shi masani ne game da komai, babu abin da yake wuce shi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Tsananin mayen mutuwa, da kuma gazawar mutum ya kare kansa daga gare shi. 2 - Asali shi ne mutum ba zai iya ganin Mala'iku ba, sai dai idan Allah ya ga dama saboda wata hikimar. 3 - Sunayen Allah: (Al-auwal, Al-akhir, Azzahir, Albaxin) sun suna nuna girman Allah, da halarto da shi, a lokacin da mutum yake yin aiki na fili ko na voye.**

هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ
عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ يَعۡلَمُ مَا يَلِجُ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا يَخۡرُجُ مِنۡهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ
ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعۡرُجُ فِيهَاۖ وَهُوَ مَعَكُمۡ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ
بَصِيرٞ ٤ لَّهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَإِلَى ٱللَّهِ تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ
٥ يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِۚ وَهُوَ عَلِيمُۢ بِذَاتِ
ٱلصُّدُورِ ٦ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَأَنفِقُواْ مِمَّا جَعَلَكُم
مُّسۡتَخۡلَفِينَ فِيهِۖ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَأَنفَقُواْ لَهُمۡ أَجۡرٞ كَبِيرٞ ٧
وَمَا لَكُمۡ لَا تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلرَّسُولُ يَدۡعُوكُمۡ لِتُؤۡمِنُواْ بِرَبِّكُمۡ وَقَدۡ
أَخَذَ مِيثَٰقَكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٨ هُوَ ٱلَّذِي يُنَزِّلُ عَلَىٰ عَبۡدِهِۦٓ
ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ لِّيُخۡرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ بِكُمۡ
لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٩ وَمَا لَكُمۡ أَلَّا تُنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ لَا يَسۡتَوِي مِنكُم مَّنۡ أَنفَقَ مِن قَبۡلِ ٱلۡفَتۡحِ
وَقَٰتَلَۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡظَمُ دَرَجَةٗ مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُواْ مِنۢ بَعۡدُ وَقَٰتَلُواْۚ
وَكُلّٗا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ١٠ مَّن ذَا
ٱلَّذِي يُقۡرِضُ ٱللَّهَ قَرۡضًا حَسَنٗا فَيُضَٰعِفَهُۥ لَهُۥ وَلَهُۥٓ أَجۡرٞ كَرِيمٞ ١١



**(4) Shi ne wanda ya halicci sammai da qassai a cikin kwana shida, sun fara da ranar Lahadi, suka qare da ranar Juma'a, kuma shi mai ikon halittarsu ne a qasa da qiftawar ido, sannan ya xaukaka a kan al'arshi, xaukakar da ta dace da shi. Ya san duk abin da yake shiga cikin qasa, na ruwan sama, da irin qwaya, da makamantan su, kuma ya san abin da yake fitowa daga cikin qasar, na daga tsirrai da ma'adinai, da makamantan su, kuma ya san abin da yake saukowa daga saman, na daga ruwan sama, da wahayi, da makamantan su, kuma ya san me yake hawa saman na daga Mala'iku, da ayyukan bayi, da rayukansu. Yana tare da ku - Ya ku mutane - a duk inda kuka kasance da iliminsa, babu wanda yake vuya a gare shi daga cikinku. Allah mai gani ne da abin da kuke aikatawa, babu wani abu da yake vuya a gare shi daga cikin ayyukanku, kuma sai saka muka a kansu.**

**(5) Shi kaxai yake da mulkin sammai da qassai, kuma gare shi ne kaxai ake mayar da al'amura, sai ya yi wa halitta hisabi a ranar alqiyama, ya saka musu a kan ayyukansu.**

**(6) Yana shigar da dare a cikin yini, sai duhu ya zo, mutane su yi barci, kuma yana shigar da yini a cikin dare, sai haske ya zo, sai mutane su fita zuwa wuraren ayyukansu. Shi masanin abin da yake cikin qirazan bayinsa ne, babu abin da yake vuyar masa daga ciki.**

**(7) Ku yi imani da Allah, kuma ku yi imani da Manzonsa, kuma ku ciyar daga dukiyar da Allah ya sanya ku mamaya a kanta, kuna sarrafata daidai da yadda Allah ya shar'anta muku, waxanda suka yi imani da Allah daga cikinku, kuma suka bada dukiyoyinsu a tafarkin Allah, suna da lada mai girma a wurin Allah, shi ne Aljannah.**

**(8) Mene ne dalilin da zai hana ku yin imani da Allah?! alhali Manzo yana kiran ku zuwa ga Allah, domin kwaxayin ko zaku yi imani da Ubangijinku, tsarki ya tabbata a gare shi, kuma Allah ya yi alqawari da ku a kan zaku yi imani da shi, a lokacin da ya fito da ku daga tsatson iyayenku, idan har da gaske kuke yi, ku Muminai ne.**

**(9) Allah shi ne wanda yake saukar wa da bawansa Muhammad (S.A.W) ayoyi bayyanannu, domin ya fitar da ku daga cikin duhun kafirci da jahilci, zuwa ga hasken imani da ilimi. Haqiqa Allah mai tausayawa ne mai jin qai a gare ku, yayin da ya aiko muku da Manzonsa a matsayin mai shiryarwa, kuma mai yi muku bushara.**

**(10) Kuma wane dalili ne zai hana ku ciyarwa a tafarkin Allah?! Alhali gadon sammai da qassai duk na Allah ne. kuma wanda ya ciyar da dukiyarsa saboda Allah, da neman yardarsa daga cikinku – Ya ku Muminai – tun gabanin a buxe Makkah, kuma ya yaqi kafirai, don taimakon musulunci, ba zai yi daidai da wanda ya ciyar da dukiyarsa bayan buxe Makkah, kuma ya yaqi kafirai ba. Waxancan da suka ciyar kafin buxe Makkah, kuma suka yi yaqi a tafarkin Allah, su ne mafiya girman matsayi da daraja a wurin Allah, fiye da waxanda suka ciyar da dukiyarsu saboda Allah bayan buxe Makkah, kuma suka yaqi kafirai. Haqiqa Allah ya yi wa duka vangarorin biyu alqawarin Aljannah. Kuma dangane da abin da kuke aikatawa Allah masani ne mai bada labari, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikin ayyukanku, zai kuma saka muku a kansu.**

**(11) Wane ne zai bada dukiyarsa a cikin daxin rai saboda Allah, sai Allah ya ba shi ladan abin da ya ciyar tare da ninka masa, kuma a ranar alqiyama yana da lada mai girma, shi ne Aljannah?!**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Dukiya duk mallakar Allah ce, shi kuwa mutum ajiyar ta aka ba shi.**
**2 - Fifikon darajar Muminai yana tabbata ne da rigaye zuwa ga imani da ayyuka nagari.**
**3 - Ciyar da dukiya a tafarkin Allah, yana haifar da albarka da qaruwar dukiya.**

يَوْمَ تَرَى الْمُؤْمِنِينَ وَالْمُؤْمِنَاتِ يَسْعَىٰ نُورُهُم بَيْنَ أَيْدِيهِمْ
وَبِأَيْمَانِهِم بُشْرَاكُمُ الْيَوْمَ جَنَّاتٌ تَجْرِي مِن تَحْتِهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ
فِيهَا ذَٰلِكَ هُوَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ١٢ يَوْمَ يَقُولُ الْمُنَافِقُونَ وَالْمُنَافِقَاتُ
لِلَّذِينَ آمَنُوا انظُرُونَا نَقْتَبِسْ مِن نُّورِكُمْ قِيلَ ارْجِعُوا وَرَاءَكُمْ
فَالْتَمِسُوا نُورًا فَضُرِبَ بَيْنَهُم بِسُورٍ لَّهُ بَابٌ بَاطِنُهُ فِيهِ الرَّحْمَةُ
وَظَاهِرُهُ مِن قِبَلِهِ الْعَذَابُ ١٣ يُنَادُونَهُمْ أَلَمْ نَكُن مَّعَكُمْ قَالُوا بَلَىٰ
وَلَٰكِنَّكُمْ فَتَنتُمْ أَنفُسَكُمْ وَتَرَبَّصْتُمْ وَارْتَبْتُمْ وَغَرَّتْكُمُ الْأَمَانِيُّ
حَتَّىٰ جَاءَ أَمْرُ اللَّهِ وَغَرَّكُم بِاللَّهِ الْغَرُورُ ١٤ فَالْيَوْمَ لَا يُؤْخَذُ مِنكُمْ
فِدْيَةٌ وَلَا مِنَ الَّذِينَ كَفَرُوا مَأْوَاكُمُ النَّارُ هِيَ مَوْلَاكُمْ
وَبِئْسَ الْمَصِيرُ ١٥ ۞ أَلَمْ يَأْنِ لِلَّذِينَ آمَنُوا أَن تَخْشَعَ ثلاثة أرباع الحزب ٥٤
قُلُوبُهُمْ لِذِكْرِ اللَّهِ وَمَا نَزَلَ مِنَ الْحَقِّ وَلَا يَكُونُوا كَالَّذِينَ
أُوتُوا الْكِتَابَ مِن قَبْلُ فَطَالَ عَلَيْهِمُ الْأَمَدُ فَقَسَتْ قُلُوبُهُمْ وَكَثِيرٌ
مِّنْهُمْ فَاسِقُونَ ١٦ اعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ يُحْيِي الْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا قَدْ بَيَّنَّا
لَكُمُ الْآيَاتِ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ١٧ إِنَّ الْمُصَّدِّقِينَ وَالْمُصَّدِّقَاتِ
وَأَقْرَضُوا اللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا يُضَاعَفُ لَهُمْ وَلَهُمْ أَجْرٌ كَرِيمٌ ١٨



**(12) Ranar da zaka ga Muminai maza, da Muminai mata haskensu yana tafiya a gabansu, da damansu, kuma a wannan rana za a ce da su: "Ana yi muku albishir da Aljannatai waxanda qoramu suke gudana ta qarqashin gidajensu da bishiyoyinsu, kuma zasu zauna a cikinsu har abada, wannan sakamakon shi ne babban rabo, wanda babu rabon da ya kai shi.**

**Yayin da Allah ya ambaci halin Muminai a wannan rana, sai kuma ya ambaci halin da munafukai zasu samu kansu a ciki ya ce:**

**(13) Ranar da munafukai maza da munafukai mata zasu cewa waxanda suka yi imani: "Ku jira mu, ko ma xosana daga haskenku, yadda zamu samu mu tsallake siraxi". Sai a ce munafukai ana musu izgili: "Ku koma bayanku, ku nemi hasken da zaku haska da shi, sai a buga wata katanga a tsakaninsu, wannan katanga tana da qofa, ta cikinta vangaren da muminai suke akwai rahama a ciki, da bayanta kuwa inda munafukai suke akwai azaba a ciki.**

**(14) Munafukai suna kiran Muminai suna cewa: "Shin ba tare da ku muke ba, a cikin Musulunci da xa'ar Allah?!" Sai musulmai su basu amsa da cewa: "Hakane, kun kasance tare da mu, sai dai ku kun fitini kawunanku da munafunci, kuka halakar da kanku, kuma kuka yi dakon muminai a samu nasara a kansu ku bayyana kafircinku, sannan kuka yi shakka a taimakon Allah ga muminai, da tashi bayan mutuwa, burace burace na qarya suka ruxe ku, har sai da mutuwa ta zo muku kuna kan haka, kuma shaixan ya ruxe ku ga barin Allah.**

**(15) Ya ku Munafukai, a yau ba za a karvi fansa daga gare ku ba a kan azabar Allah, kuma ba za a karvi fansa daga waxanda suka bayyana kafircinsu ba, makomar ku da makomar kafirai ita ce wuta, ita ce tafi dacewa da ku, kuma kuka fi dacewa da ita, makoma ta yi muni.**

**(16) Shin lokaci bai yi ba ga waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, zukatansu su yi laushi su samu nutsuwa da ambaton Allah ba, da abin da ya sauka daga Alqur'ani na alqawarin lada ko alqawarin azaba. kuma kada su kasance kamar waxanda aka basu Attaura daga cikin Yahudawa, da waxanda aka basu Injila daga cikin Nasara, a wurin qeqashewar zuciya, kuma sannan zamani ya yi tsawo tsakaninsu da aiko Annabawan su, sai zukatansu suka qeqashe saboda haka, mafiya yawansu masu fita ne daga xa'ar Allah zuwa savonsa?!.**

**(17) Ku sani Allah yana raya qasa ta hanyar fitar da tsironta bayan ta bushe, mun bayyana muku hujjoji a kan ikon Allah, da kaxaitakarsa – Ya ku mutane - don ku hankalta, ku san cewa wanda yake raya qasa bayan mutuwarta mai iko ne a kan ya tayar da ku bayan mutuwarku, kuma mai iko ne ya sanya zukatanku su yi laushi bayan sun qeqashe.**

**(18) Haqiqa masu yin sadaka a cikin maza da wani vangare na dukiyarsu, da masu yin sadaka a cikin mata da wani vangare na dukiyarsu, waxanda suke ciyar da dukiyar ta su cikin daxin rai, ba tare da yin gori ko cutarwa ba, za a ninka musu ladan ayyukansu, kyakkyawa xaya lada goma, har zuwa ninki xari bakwai, har zuwa ninki da yawa, kuma a tare da haka suna da wani ladan mai girma a wurin Allah, shi ne Aljannah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kyautar Allah ga Muminai, ta yadda zai basu haske yana tafiya a gabansu da damansu.**
**2 - Savon Allah da munafunci sababi ne da yake kawo duhu da halaka ranar alqiyama.**
**3 - Jiran faruwar wani mummunan abu ga muminai da shakka a kan tashi bayan mutuwa, da ruxuwa da burace burace, da ruxuwa da Shaixan duk yana cikin siffofin munafukai.**
**4 - Haxarin rafkana mai kaiwa zuwa ga qeqashewar zuciya.**

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَۖ وَٱلشُّهَدَآءُ
عِندَ رَبِّهِمۡ لَهُمۡ أَجۡرُهُمۡ وَنُورُهُمۡۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ
بِـَٔايَٰتِنَآ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١٩ ٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا ٱلۡحَيَوٰةُ
ٱلدُّنۡيَا لَعِبٞ وَلَهۡوٞ وَزِينَةٞ وَتَفَاخُرُۢ بَيۡنَكُمۡ وَتَكَاثُرٞ فِي ٱلۡأَمۡوَٰلِ
وَٱلۡأَوۡلَٰدِۖ كَمَثَلِ غَيۡثٍ أَعۡجَبَ ٱلۡكُفَّارَ نَبَاتُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ
مُصۡفَرّٗا ثُمَّ يَكُونُ حُطَٰمٗاۖ وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٞ شَدِيدٞ وَمَغۡفِرَةٞ
مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٞۚ وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا مَتَٰعُ ٱلۡغُرُورِ ٢٠
سَابِقُوٓاْ إِلَىٰ مَغۡفِرَةٖ مِّن رَّبِّكُمۡ وَجَنَّةٍ عَرۡضُهَا كَعَرۡضِ ٱلسَّمَآءِ
وَٱلۡأَرۡضِ أُعِدَّتۡ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ
ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ٢١ مَآ أَصَابَ
مِن مُّصِيبَةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِيٓ أَنفُسِكُمۡ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مِّن
قَبۡلِ أَن نَّبۡرَأَهَآۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٢٢ لِّكَيۡلَا
تَأۡسَوۡاْ عَلَىٰ مَا فَاتَكُمۡ وَلَا تَفۡرَحُواْ بِمَآ ءَاتَىٰكُمۡۗ وَٱللَّهُ
لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخۡتَالٖ فَخُورٍ ٢٣ ٱلَّذِينَ يَبۡخَلُونَ وَيَأۡمُرُونَ
ٱلنَّاسَ بِٱلۡبُخۡلِۗ وَمَن يَتَوَلَّ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡغَنِيُّ ٱلۡحَمِيدُ ٢٤



**(19) Waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi imani da Manzanninsa ba tare da sun rarrabe tsakaninsu ba, waxannan su ne masu gaskiya na haqiqa. Shahidai kuma suna da wani lada mai girma a wurin Ubangijinsu wanda ya tanada musu shi, kuma suna da haske mai tafiya a gabansu da daman su a ranar alqiyama. Waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa, suka qaryata ayoyin da aka saukar wa Manzon mu, waxannan su ne 'yan wuta, zasu shige ta a ranar alqiyama, zasu dauwama a cikinta, baza su fito daga cikinta ba.**

**(20) Ku sani rayuwar duniya ba komai ba ce face wasa, da jiki yake yi, da shagala da zuciya take yi, da alfahari a tsakaninku da abin da yake cikinta na mulki da jin daxi, da tinqaho da yawan dukiya da 'ya'ya. Misalinta kamar misalin ruwan sama ne wanda yabanyarsa ta yi kyau, ta qayatar da manoma, sannan wannan shukar bata xauki wani tsawon lokaci ba tana koriya shar sai ta bushe, sai ka ga tana yin ja bayan da tana kore, sannan sai Allah ya mayar da ita karmami mai karyewa. A lahira akwai azaba mai tsanani ga kafirai da munafukai, da gafarar zunubai daga Allah ga bayinsa Muminai, da yardarsa. Rayuwar duniya ba komai bace face wani jin daxi mai gushewa, don haka duk wanda ya fifita daxi mai gushewa a kan ni'imar lahira tabbas ya yi asara kuma ya cuci kansa.**

**(21) Ya ku mutane ku yi gaggawa zuwa ga ayyuka nagari, wanda zaku samu gafarar zunuban ku ta hanyar aikata su, daga tuba, da waninta daga cikin ayyukan qwarai, domin ku samu Aljannar da faxinta kamar faxin sammai da qassai. Wannan Aljannar Allah ya tanade ta ga waxanda suka yi imani da shi, da Manzanninsa. Wannan sakamako falala ne daga Allah yake bada ita ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, Allah mai tsarki ma'abocin falala ne mai girma ga bayinsa Muminai.**

**(22) Babu wata musiba da zata samu bayi a bayan qasa, kamar fari ko waninsa, haka nan kuma babu wata musiba da zata samu bayi su kansu face dama an riga an rubuta ta a cikin Lauhul Mahfuz, tun kafin mu halicci halitta, kuma wannan abu ne mai sauqi a wurin Allah.**

**(23) Kuma wannan domin kada ku samu damuwa game da abin da kuka rasa, kuma don kada ku yi alfahari da abin da aka baku na ni'ima, alfahari na girman kai, haqiqa Allah baya son duk mai girman kai, mai yi wa mutane alfahari da abin da Allah ya ba shi.**

**(24) Waxanda suke yin rowa da abin da ya wajaba su bayar, kuma suke umartar mutane da yin rowa, waxannan sun yi asara. Duk wanda ya bada baya ga yi wa Allah xa'a, to ba zai cutar da Allah ba, kansa kawai zai cutar. Haqiqa Allah shi ne Mawadaci, baya buqatar xa'ar bayinsa, kuma shi ne abin yabo a kowane hali.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Gudun duniya da abin da yake cikinta na sha'awa, da kwaxaitar wa ga lahira da abin da yake cikinta na ni'ima daumammiya, duk suna taimakawa wurin bin tafarki madaidaici.**

**2 - Wajabcin imani da qaddara.**

**3 - Daga cikin fa'idojin imani da qaddara shi ne kada mutum ya riqa damuwa a kan wani abu da ya rasa na rabon duniya.**

**4 - Rowa da yin umarni da ita, xabi'u ne guda biyu miyagu, kuma Mumini baya siffantuwa da su.**

لَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلَنَا بِٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلْنَا مَعَهُمُ ٱلْكِتَٰبَ
وَٱلْمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلْقِسْطِ ۖ وَأَنزَلْنَا ٱلْحَدِيدَ فِيهِ
بَأْسٌ شَدِيدٌ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَلِيَعْلَمَ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥ وَرُسُلَهُۥ
بِٱلْغَيْبِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِىٌّ عَزِيزٌ ﴿٢٥﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا نُوحًا وَإِبْرَٰهِيمَ
وَجَعَلْنَا فِى ذُرِّيَّتِهِمَا ٱلنُّبُوَّةَ وَٱلْكِتَٰبَ ۖ فَمِنْهُم مُّهْتَدٍ ۖ
وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴿٢٦﴾ ثُمَّ قَفَّيْنَا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم
بِرُسُلِنَا وَقَفَّيْنَا بِعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ وَءَاتَيْنَٰهُ ٱلْإِنجِيلَ ۖ وَجَعَلْنَا
فِى قُلُوبِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ رَأْفَةً وَرَحْمَةً وَرَهْبَانِيَّةً
ٱبْتَدَعُوهَا مَا كَتَبْنَٰهَا عَلَيْهِمْ إِلَّا ٱبْتِغَآءَ رِضْوَٰنِ ٱللَّهِ
فَمَا رَعَوْهَا حَقَّ رِعَايَتِهَا ۖ فَـَٔاتَيْنَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنْهُمْ أَجْرَهُمْ ۖ
وَكَثِيرٌ مِّنْهُمْ فَٰسِقُونَ ﴿٢٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ
وَءَامِنُوا۟ بِرَسُولِهِۦ يُؤْتِكُمْ كِفْلَيْنِ مِن رَّحْمَتِهِۦ وَيَجْعَل لَّكُمْ نُورًا
تَمْشُونَ بِهِۦ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٢٨﴾ لِّئَلَّا يَعْلَمَ
أَهْلُ ٱلْكِتَٰبِ أَلَّا يَقْدِرُونَ عَلَىٰ شَىْءٍ مِّن فَضْلِ ٱللَّهِ ۙ وَأَنَّ
ٱلْفَضْلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤْتِيهِ مَن يَشَآءُ ۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلْفَضْلِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٢٩﴾



**(25) Haqiqa mun aiko Manzannin mu da hujjoji bayyanannu, da dalilai masu girma, kuma muka saukar musu da littafi, kuma muka saukar musu da ma'auni, domin mutane su tsaya da adalci, kuma muka saukar da qarfe, a cikinsa akwai tsanani sosai, da shi ne ake yin makami, kuma a cikinsa akwai amfani mai yawa ga mutane mutane wajen sana'o'insu da ayyukansu, kuma domin Allah ya bayyanawa bayi wanda zai taimake shi da gaskiya a voye. Haqiqa Allah mai qarfi ne mabuwayi, babu abin da yake rinjayar sa, kuma babu abin da yake gajiyar da shi.**

**(26) Haqiqa mun aiko Annabi Nuhu da Annabi Ibrahim, kuma muka sanya Annabta a cikin zuriyarsu, tare da littafai da aka saukar. A cikin zuriyarsu akwai shiryayye wanda aka datar zuwa ga tafarki madaidaici, amma da yawa daga cikinsu masu fita ne daga xa'ar Allah.**

**(27) Sannan muka biyo bayansu da Manzanninmu, muka riqa aiko su ga mutanensu xaya bayan xaya, muka biyo bayansu da Annabi Isa xan Maryam, muka bashi littafin Injila, kuma muka sanya tausayi da jin qai a cikin zukatan waxanda suka yi imani da shi suka yi masa biyayya, sai suka zamo masoya juna, masu jin qan junansu, amma sai suka qirqiri wuce gona da iri a cikin addininsu, don haka sai suka bar wani abin da Allah ya halatta musu, na yin aure da jin daxin duniya, alhali bamu nemi haka a wurinsu ba, kawai dai su ne suka sa kansu, saboda farar da wani abu mara tushe a cikin addini, kaxai mun nemi su da bin yardar Allah, amma ba su aikata ba, don haka sai muka waxanda suka yi imani daga cikinsu ladansu, da yawa daga cikinsu masu fita ne daga xa'ar Allah, ta hanyar qaryatawa da abin da Manzonsa Muhammad (S.A.W) ya zo da shi.**

**(28) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta musu, ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, kuma ku yi imani da Manzonsa, zai baku rabo guda biyu na lada, ladan yin imani da Annabi Muhammad (S.A.W) da ladan yin imani da Annabawan da suka gabata, kuma ya sanya muku haske, wanda zaku shiryu da shi a rayuwarku ta duniya, kuma ku haska da shi a kan siraxi ranar alqiyama, kuma ya gafarta muku zunubanku, ya rufe su, ba zai kama ku da su ba. Allah mai tsarki mai yawan gafara ne ga bayinsa, kuma mai jin qansu ne.**

**(29) Haqiqa mun bayyana muku irin falalarmu mai girma da muka yi muku, na abin da muka tanada muku – Ya ku muminai – lada wanda ake ninka shi, don ma'abota littafi waxanda suka gabata daga cikin Yahudu da Nasara su sani cewa ba su da iko da wani abu daga falalar Allah, ta yadda za su ba wanda suka ga dama, su hana wanda suka ga dama, kuma don su sani cewa falala tana hannun Allah, yana bada ita ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa. Haqiqa Allah Ma'abocin falala ne mai girma ga wanda ya keve daga cikin bayinsa, wanda ya ga dama.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ita gaskiya dole ne ta samu wani qarfi da zai bata kariya, kuma ya yaxa ta.**
**2 - Bayanin matsayin adalci a cikin shari'ar da Allah ya saukar.**
**3 - Alaqar jini da waxanda suka yi imani bata amfana wa mutum komai matuqar shi bai yi imani ba.**
**4 - Bayanin haramcin qirqirar wani abu a cikin addini.**